[5/12, 11:27 AM] Abidah: *NAZBEER*
🌷🌷🌷
*Written by*
*Zainab Laminu Sani*
(*Abeedah*)✍️

Follow this link to join my WhatsApp group: https://chat.whatsapp.com/FP7D2LzvLM6Asy82NpHTIF

My channel 👇

Follow the NAZBEER FANS CLUB channel on WhatsApp: https://whatsapp.com/channel/0029VbAxsXB7IUYWz4OBH713

---

*FIRST CLASS WRITER'S ASSOCIATION*
(*Home of Qualities And trusted writer's of the Nition*)☀️☀️☀️

*SHIMFIƊA*

Wannan labarin ƙagaggen labari ne, banyi shi dan wani ko wata ba, duk wanda suna ko hali ya zo ɗaya arashi ne, labarin *NAZBEER* labari ne daya ƙunshi tarin abubuwa, kama daka kan zazzafar soyayya, haɗi da cin amana, makirci da kuma sarƙaƙiya, ba zanyi muku alƙawarin farin ciki ko akasin zalla ba, haka zalika tafiyace miƙaƙƙiya, kudai mu tattaro mu haɗe acikin labarin dan jin abinda ciki, fatana dai shine ku karɓi labarin da hannu bibbyu. Na gode

*MU ANTAYA CIKIN LABARI*💃💃💃

*PAGE*____ 1

Bismillahirrahmanirrahim.

Tafe take adajin sai zabga uban sauri take kai kace sama zata tashi, hankalinta a matuƙar ƙololuwar tashe, ta ko kallon gabanta, burinta shine bai wuce ta ganta a gaban Boka Darmuuje

ba.

Wata nannauyar ajiyar zuciya tasauke saboda hango bukkar Boka Darmuuje, tana ƙarasawa bata jira komai ba takutsa kanta cikin bukkar, ganinta yasa Boka Darmuuje yakwashe da wata mahaukaciyar dariya, wanda aƙalla Sai data ɗauki adadin mintuna biyar bata gushe ba, baƙar fuskarsa me ban tsoro ya haɗe yana kallonta da ƙwala-ƙwalan idanunsa masu kamar gauta.

"Kinyi kuskuren barin yabanyar araye, da'ace tun wancan lokacin kinyi abinda mukace ba tare da kuskure ba, da aikin ki bai lalace ba". Ya faɗi da muryarsa me amo mara daɗin sauraro.

"Ba haka muka yi da kai ba, ya kai sarkin Bokaye, tun waccen lokacin na sanar dakai cewa na gusar da yabanyar kuma allon tsafi yanuna hakan, Kuma yanzu kacemin haka?, kada ƙwarin gwiwar da nake dashi akanka ya zama na banza".

Wata razananniyar tsawa aka dakamata damurya maradad'in sauraron, Boka Darmuuje da yake sakin gurnani mara dad'in ji ya kalle ta da jajayen idanunsa, "Balaraba!". ya kira Sunan ta da murya me amo, a razane ta ɗago ta dube shi, jin yadda ya kira Sunan nata.

"Balaraba, kin sanni kinsan abinda zan iya aikatawa, ba tun yau ba muke tare dake, badan mahaifiyar ki ba danayi miki abinda biki tsammata, ke muka ba zaɓi Kuma kika zaɓi wanda yayi miki,
amma kamr yadda na faɗa albarkaci mai ƙosai mahaifiyarki kika ci, dan haka ki tashi ki koma zamu sabunta aiki akanshi, har abada bazai sake tuna ta ba balle ma abinda ke tare da ita".

Wata nannauyar ajiyar zuciya ta sake saukewa sannan ta miƙe ta fice daka bukkar.

A can kuwa ɗaya ɓangaren
Inna Hadiza ce tsaye akan mahaukaciyar matar da duk da tsananin haukan da ta ke ciki jaririyar ƴarta sabuwar haihuwa tana hannuta ta matseta a ƙirjita ƙam, cike da tausayawa Inna Hadiza ke kallon mahaukaciyar matar, "Baiwar Allah ba cutar da ita za mu yi ba, zan mata wanka ne, ke ma kisamu kiyi kici abinci". Ta faɗi cikin tausayawa, domin har ga Allah matar tausayi take bata.

Shiru mahaukaciyar tayi tana saurarar Inna Hadiza kamar tana fahimtar abinda take cewa, idonta tamayar akan kyakykyawar ƴar tata itama shiru tayi tana kallon ta kamar maitunanin bada ita, idonta ta ɗago tasake kallon Inna Hadiza saita sake kallon jaririyar ta, Baba Halliru da yake tsaye yana kallon duk abinda ke faruwa yayi magana a sanyaye.

"Hadiza ƙyaleta, wata ƙila bata yarda damu bane, tana ganin kamar zamu cutar da itane, daka ganin alamun ta kinsan akwai abinda ke damunta".

Inna Hadiza taɗago ta kalleshi "Ba yarda ne ba ta yi da mu ba, tantamar bamu yarinyar take yi,

don tana ganin zamu iya guduwa da ita".

Jinjina kai Baba Halliru yayi, shima yana durƙusawa a gabanta yace "Baiwar Allah ba cutar da ke za mu yi ba, ko wani muka ga zai cutar da ke sai inda ƙarfin mu ya ƙare".

Ga mamakinsu sai suka ga tayi murmushi tana miƙo masu yarinyar, Inna Hadiza jiki na rawa ta miƙa hannunta ta amshi jaririyar.

"Tabarakallahu masha Allah". Ta faɗi ganin tsananin kyawun da yarinyar, ta ɗago ta dubi Baba Halliru tace "Malam zo ka ga yarinyar,kyawu kamar ƴar larabawa".

Shima amsar yarinyar yayi yana dubanta, "Gashi bamu san ko mai game da matar nan ba, kuma ga dukkan alamun bata magana, balle musan dunan yarinyar". Yayi maganar cike da jimami.

"Malam kai mata huɗuba da Abida kawai". Faɗin Inna Hadiza, Murmushi yayi yace "Allah ya raya Abida". itama murmushin tayi da cewa "Ameen".

*Abuja Nigeria* *ASOKOTO G.R.A*

wasu lafifayyun motoci ne,suke fitowa daga cikin wani layi, kai daka ganin motocin kasan mamallakin su yaci ya tada Kai.

Ɗaya daka cikin motocin data kasance kalar baƙa na leƙa dan ganin wanne gwarzon ne a ciki, ba kowa na gani ba face shahararren matashin nan mai ji da kuɗi da lokaci wanda ƴan uwan sa matasa suke masa laƙani da young millonian wato NAZEER BASHIR RIMI C.E.O NA company NAZBEER INVESTMENT NIGERIA LIMITED.

Company nin da yake fitar da kayan masarufi wanda yana daga cikin manya company nin da muke dashi anan nahiyar Africa.
wanda suke da manyan rassa a nan Abuja da Lagos da sauran manya hajohin Nigeria, dama ƙasashen ƙetare.

Motocin nasa basu tsaya ko ina ba sai a babbar harabar company nin sa, ma'aikatace babba da aka yi mata gini na zamani, domin kuwa kusan rabin ginin anyishi da glass ne.

Gad ɗin shine suka fito suka zagaye motar da yake ciki, kai kace zasu iya hana malaikan

ɗaukar rai zuwa inda ya ken.

Ɗaya ne ya matsa kusa da murfin motar ya kama handil ɗinn motar ya buɗe haɗi da ja baya, dan bawa na ciki damar fitowa.

Sai da aka ja kusan minti uku kafin mutumin dake cikin motar ya ziro  da kyawawan fararen ƙafafunsa sanye cikin wani silba ɗin takalmi rufaffu,Sai da ya ƙara jan wasu mintocin da zasu iya kaiwa biyar sannan ya fito gaba ɗayansa.

"Ma sha Allah".  Na faɗa domin ganin tsantsar kyawun da ubangiji yayi masa, kamar shi yayi kansa, fari ne sosai irin farin da zaka rantse bai haɗa jiƙo da Africa ba, saye yake da suit kalar blue me duhu, sosai kayan suka dace da kalar kyakykyawar fatarsa da hutu ya ratsata, idanunsa saye cikin farin siririn farin glass daya fito da asalin kalar shuɗiyar ƙwayarsu, kwantaccen sajensa ya kwanta luff, sosai yayi kyau kamar ka sace shi la gudu.

Takawa ya fara yi cike da sadaukantaka, ko wanne taku yana  fito da asalin jarumtarsa, a hankali ya ke sauke ƙafafun nasa bisa ƙasa,

 Kallon sa ya kai akan agogon dake ɗaure a tsintsiyar hannunsa wanda sai yanzu ne  na lura dashi, agogone mai azabar kyau, na companynin Rolex.

"TAHIR". Ya kira sunan P.A ɗin shi a hankali kamar me tsoron yin magana, cikin hanzari da zafin nama TAHIR ɗin ya matso kusa da shi, "Sir!".

Ya faɗi cike da girmamawa, "Ina buƙatar ganin file d'in kayan da aka fitar jiya na office ɗicn KHALIL".  Yayi maganar babu alamar wasa a tare dashi,"Okay  boss!".  Ya faɗa yana mai bin wata hanyar daban ba wacce suke ba, cikin takunsa me girgiza zukatan mahassada ya cigaba da ratsa companyn, Kai tsaye lifta ya shiga don ta sadashi da office ɗin shi dake hawan ƙarshe, mintuna ƙalilan liftar ta tsaya a dai-dai ƙofar office ɗin na shi dake maƙale da sunansa NAZEER BASHIR RIMI.

ƙofar office ɗin da takasance ta gilas ya nufa, a gaban ƙofar ya tsaya, sakon ɗaya biyu, ƙofar  ta zuge kanta ya wuce, sassayanan k'amshin air freshener da sanyin A.C suka had'u suka bada yanayi me dad'i, a hankali ya taka har cikin office ɗin daya gama k'awatuwa da kayan k'awa, gaban kujerarsa ya Isa ya zauna, idanu ya lumshe yana juya kujerar a hankali hannunsa a saman goshinsa, idonsa ya bud'e hankali ya sauke a kan makeken hoton iyayenaa dake sak'ale a gefen teburin nasa, wani ya d'an matse a tsakanin k'irjinsa, tunawa da Umminsa da kuma halin data ke ciki. "Allah ya baki lafiya ummina". Ya fad'i a saman labbansa.

Share and comment my lovely fans❣️❣️❣️

Taku har kullum

Abeedah.....✍️
[5/12, 8:27 PM] Abidah: Follow this link to join my WhatsApp group:
https://chat.whatsapp.com/J9oI2KIySOW3LbV89O51aJ
---------------------------------------
My channel 👇
Follow the NAZBEER FANS CLUB channel on WhatsApp:
https://whatsapp.com/channel/0029VbAxsXB7IUYWz4OBH713
---------------------------------------

*FIRST CLASS WRITER'S ASSOCIATION*

(*Home of Qualities And Trusted writer's of the Nation*)☀️☀️☀️

*PAGE*------- 2

Bismillahirrahmanirrahim.

Katafaren manshion ne me ɗauke da mabanbantan al-uma da suke rayuwa a cikin sa,  mutane ne da zasu kai kimanin 7 suke ta kai kawo a farfajiyar manshion ɗin, wanda kallo guda zaka yi ka shaida ƴan aiki ne, sanye suke cikin tufafi iri guda, kalar baƙi da fari, shi ne tufafin masu aikin gidan mazansu da matansu.

Bayan wata ƴar budurwar nabi ganin ta nufi wata ƙofa, da alama itace ƙofar data sadaka da cikin babban falon dake ɓangaren hagu daka cikin jerin gine-ginen da suke iri guda.

Nima sai na shiga dan ganin me ake yi  a sashen, ido na lumshe dan ganin irin tsaruwar falon, sosai aka narka dukiya a cikinsa, kujerun falon kalar jajaye ne da adon ruwan zinare, hakan yasa komai na adon falon ya kasance ja da ruwan zinaren.

🌷 Idona ne yayi tozali da wata hamshaƙiyar mace wacce aƙalla zata kai shekaru 40_41, sanye take da farin lashi wanda yaji adon duwatsu koraye, kai daka gani kasan me tsada ne,

idonunta sakaye cikin wani siririn farin glashi, laptop ce a saman cinyarta tana daddan nawa, BARISTA NA'IMA ISMA'IL RIMI ke nan.

Ɗago idon ta tayi ta sauke kan budurwar dake zaune a kujerar gefen ta, "Rukayyah baki ji ana sallah bane?". Barista tayi maganar idonta akan Rukayyan, budurwar da aka kira da Rukayyah ta ɗago kai ta kalli Barista, "Naji mana".

Tayi maganar tana cigaba da danna wayarta, haɗi da jan guntun tsaki, "Ni kikewa tsaki Rukayyah?". Barista tayi maganar tana jinjina rashin kunya irinta Rukayyan, baki Rukayya ta tura, "Wallahi zama da Mami takura ne".

Tayi maganar ciki-ciki, hakan yasa Barista bata ji abin da take faɗi ɗin ba, Miƙewa Rukayya tayi da nufin barin gurin, ƙarar takun data ji daka sama yasa ta tsaya, Hajiya Kulu ce take sakkowa daka d'aya daga cikin matattakalar benen da suke guda uku a falon, 🌷
sakkowa tayi gaba d'aya da d'an hanzarin ta, "Saurin riƙo hannun Ruƙayya". "Me ke faruwa?". Tayi tambayar idonta akan Barista.

Baki Ruƙayya ta tura, "Mami ce". "Wai dan Allah ke kam NA'IMA me yasa kike son takurawa yaran nan ne?, wannan masifa har ina?, kin kaso auren ki shi ne bari ki zo ki takurawa yaran masu gida ko?, to wallahi ba zai saɓu ba sam". Tayi maganar tana ƙanƙance ido tana duban Barista, masifa take kamar zata cinyeta.

Hargagin Hajiya Mama ne ya fito da sauran jama'ar gidan, kowa ya fito sai dai ya koma gefe ɗaya, don ba wanda zai iya da masifar Hajiya Maman.

Alha Sulaiman ne ya fito zai yi magana ke nan sai ga yayansa Alhaji Mutallab Shi ma hayaniyar tasa ya fito, "Me ke faruwa ne?".

Yayi maganar yana duban Alhaji Sulaiman, "Wallahi Yaya nima fitowa ta ke nan".

"Hamma Bashir baya nan ne?". Tsaki ya ja me sauti, "To ina zaka gan shi, yana can gurin waccen matar tashi mana".

Gaban Hajiya Mama dake ta sababi Alhaji Mutallab da suke kira da Abi ya isa, mugun kallon da ya aika mata yasa ta haɗiye sauran maganar dake bakin ta, badan taso ba, dan tana mugun shakkar mijin nata.

"Menene haka kike yi Kulu?, ƴar uwar tawa zaki tasa a gaba kina cin mutumci?".

Juyawa ya yi ya kalli sauran jama'ar dake gurin,
"Kowa ya wuce in da za shi".

Da ɗai-ɗai da ɗai-ɗai suka fice a falon,
kowa da abinda ke bakin shi dan, ba hakan suka so wasan ya tsaya ba.

Sun so suga yadda za'a ƙare wasan, haka dai kowa ya koma sashensa.

Shi kuwa bawan Alhaji Bashir yana can gurin matar shi, farin cikin shi, uwar ƴaƴan shi, wadda jarabawar lalura ta sameta .

*Abuja Nigeria*

*DAKWA*
*Abida*

🌷🌷🌷

Gida ne irin babban gidan nan, wata kyakykyawar budurwa da ba zata wuce shekaru sha 17 ba na hanga zaune bisa kujera ƴar tsuguna, saman cinyarta faranti ne tana tsintar shinkafa,

Daga cikin ɗaki Inna Hadiza ce take cewa "Abida wai har yanzu biki gama tsintar bane?". "Inna na kusa fa, shinkafar shagon Audu bata da kyau, shiya sa nace ki kawo naje bakin titi na sayo, kika ce a'a". Tayi maganar cikin sanyin da take ɗabi'arta, Inna Hadiza tace "Oh!, ni ƴasu, ke kam mita kamar tsohuwar data gaji da duniya". Daariya tayi tace "Kai Inna, ni ɗin?". "Ke kuwa".

Miƙewa tayi bayan ta gama tsintar shinkafar, "Inna bari na duba Ammita". "To, sai kin dawo, ki bi a hankali". "To Inna" Abida ta amsa tana ƙarasa saka hijabinta ta fice, a ƙofa taci karo da Inna Laure, "Za'a tafi yawon ta zubar ɗin ne?".

Wani abu ya tokare maƙoshin Abida, domin har ga Allah, ta tsani wannan kalmar da su Inna Laure ke dan gantamata, ba tare da tankawa Inna Lauren ba tasa kai ta fice tana ɗauke ƙwallar data faɗo mata.

"Ai kinsan ana fakewa da duba wannan mahaukaciyar uwar tata tana gantalinta". Inna Halime ta karɓe zancen,🌷

Ina tafe ina sharar hawaye, na rasa me na tarewa waɗannan bayin Allah, da suka ɗauki kara tsana suka ɗora min, sun yanke duk wata alaƙa da zata haɗani da ƴaƴansu, farin cikin shima

suna so su daƙile min shi, sun mata cewa ko wanne ɗan Adam baya wuce ƙaddararsa, tabbas da ace ɗan Adam yana dana ikon tsarawa kansa rayuwa da ban tsarowa tawa rayuwar haka ba, sai dai ƙaddarata ta riga fata, Allah shine me tsarawa bawansa abinda ya dace dashi, kuma yana sane dani da mahajfiyata da ya tsaro mana haka a cikin littafin ƙaddararmu.

Allah ya sani bani da wani bango ko madogara face waɗannan bayin Allah, Inna Hadiza da mijinta Baba Halliru.

A yanzu bani da wani buri na samun lafiyar mahaifiyata, kullum na ɗaga hannu lafiya nake roƙa mata a gurin Allah.

"Ku ko dan Allah me yasa kuke haka?, na rasa me yarinyar nan ta tare muku a rayuwa da kuka tsangwa meta?".

Baki suka taɓe hadi da cako kallabi gaba, Inna Laure ce ta gatsine fuska tace "Fili da yawa mana Hadiza, nan naga muna zaman zamanmu kuka ɗakko mana wannan annobar dangin mayu, ai daka gani kinsan sun haɗa iri da mayu, wannan kyawu kamar ita tayi kanta".

Aiko Inna Halime ta karɓe, "Wallahi kam, wama ya sani ko a can dangin nasu na mayu wani ya kame kurwar mahaukaciyar Babar tata, kin san an ce wai a cikinsu ma suna ci".

"Uhmm, Allah dai ya kyauta, mudai kurwarmu kurr, maye ya ci kan shi yasha baƙin ruwa".

Inna Laure ta fadi suna tafa hannu hadi da shewa.

Kai kawai Inna Hadiza ta girgiza, da fatan Allah ya ganar da su Laure.

Ji nayi an ja hijabina ta baya, hakan yasa nayi saurin juya dan na tsorata ƙwarai, "Ke dai kin cika tsoro". Ƙawata AMINA ta fadi tana dariya, ɗan murmushi na yi mata, AMINA ita kaɗai ce ƙawata kaf layin, da ita kaɗai nake zama nayi hira har wani lokacin nakan sanar mata da damuwata.

"Ina zuwa haka da ranar nan?". "Duba Ammita zan je". "Allah sarki, ya jikin nata?". Ta tambaya, "Alhamdulillah".

"Kinga badan Mama ta aikeni ba da munje nima na dubota". "Ayya babu komai, wani lokacin sai muje".Da haka muka rabu.

Ina tafe ina tunani har na ƙarasa ƙofar gidan na Malam Salihu, Malam Salihu babban Malamin addini ne dake koyar da almajira, kuma ya kan taimakawa bayin Allah da maganin da Allah ya hore masa.

Malam Sani abokin Baba Halliru shi ya bada shawarar kai Ammi gurin Malam Salihun ko Allah

zai sa a dace, dan shi magani dace ne ba'a san inda za'a dace ba, mana sa ran nasara a maganin na shi, dan ya sanar mana akwai sihiri me ƙarfi a tare da ita.

Da sallama na shiga gidan Malam ɗin, matar Malam Inna Zuwaira dake tsakar gidan ta amsani da far'a, "Lale marhabun, Abidatu kece tafe da ranar nam?".   "Ehh Inna, nazo duba jikin Ammi ne".  "Allah sarki ki shiga to".   Da "To". Na amsa cikin raina ina aiyyana kirkin matar Malam.

Ɗakin data ke kwancen na shiga, kamar koda yahshe haka na isketa kwance, haawayen tausayin ta ya gangaromin.

Har gabanta na isa, hannunta na kamo cikin nawa, ido na zuba mata, "Ammita dan Allah ki buɗe baki ki min magana ko da sau ɗaya ne".   Na faɗi muryata na rawa, ido ta zubamin kawai ba tare da tace komai ba, "Ina son sanin ɗin wacece?, kuma suwaye danginmu?, duk bani da wannan amsar, ke kaɗai ce zaki iya bani ita".

Na ƙarasa ina fashewa da kuka me tsuma zuciya, na sake tabbatarwa da mahaifiya bango ce ga rayuwar ƴaƴanta, tabbas duk wanda ya rasa mahaifiya yayi babban rashin da har abada ba zai sami madadin ta ba.

Na ɗauki tsayin lokaci ina kukan kafin na gaji dan kaina nayi shiru.

Sai da yamma liss sannan na yiwa matar Malam sallama na koma gida.

Mu haɗe daku a next page don jin cigaban labarin, labarin nan fa na faɗa muku salonsa na dabban ne.

Like an share my lovely fans, ina mugun yin ku wallahi, i love you irin wujiga-wujiga ɗin nan.🫶🫶🫶

*Taku*
*ABEEDAH*✍️
[5/13, 9:12 PM] Abidah: Follow this link to join my WhatsApp group: https://chat.whatsapp.com/J9oI2KIySOW3LbV89O51aJ
---------------------------------------

*NAZBEER*
🌷🌷🌷

*Writeen by*
*ABEEDAH*✍️

*FISRT CLASS WRITER'S ASSOCIATION*
(*Home of Qualities And Trusted writer's of the Nation)*☀️☀️☀️

*PAGE*------- 3

Bismillahirrahmanirrahim.

*KANO STATE*
*NASARAWA G.R.A*

Hajiya Balaraba

Ahankali take jan motar ta daga inda ta fakata bayan fitowar ta daga gurin boka Darmuuje, a hankali ta cigaba da ratsa kwazazzabai da duwatsun nan dake hanyar, domin kuwa ƙumgurmin dajine da me karatu ba zai taɓa tunanin wani ɗan Adam zai iya shiga cikinsa ba.

Amma saiga shi saboda neman biyan buƙatar duniya da neman a durƙusar da rayuwar baiwar Allah da bata jiba ba ta gani ba, Balaraba ta shigo shi.

Duniya ina zaki da mu ne?, wai yanzu har ɗan uwanka musulmi zai nemi ya saka ka a tsaka mai wuya, haba 'yan uwa yau shena zamu aje san zuciya da sankan mu,mudubi gaskiya mugane cewa wannan duniyar ba matabbata bace, wai a hakane muke kiran kanmu musulmai, kuma har kaje kaɗauki buta kayi alwala kaje kai sallah kana me tunanin samun rabauta a duniya da lahira.

wannan hanyar bamai ɓullewa bace da muka ɗaukarwa kanmu, ya kamata mubuɗe zukatanmu mu kalli gaskiya, mudawo kan turba tagari, wanda zamu amfanar da kanmu.

A haka ta cigaba da tafiya har tafito cikin gari, kai tsaye tahau titin da zai sadata da Nasarawa.

Hon tayi a gaban katafaren get ɗin gidan, da hanzari me gadin ya taso ya wangale mata get ɗin, hancin motar ra danna cikin gidan.

A gurin da aka tanada don ajiye motocin gidan tayi parking, cikin gidan ta nufa tana ta zabga sauri kamar zata tashi sama.

"Mami har kin dawo?". Ɗaya daka cikin ƴan matan dake zaune a falon ta faɗi tana cigaba da latsa wayar data ke yi.

Biba da bata ce komai ba tun shigowar Mamin ta kwashe da dariya, wacce ta jawo hankalin Abdul da Anas da Tijjani dake can gefe na falon suna buga gema.

"Wai Mami daka ina kike haka?, kinga fuskarki kuwa?". Biban ta faɗi har lokacin bata daina dariyar ba.

"Mami kamar wacce kura ta biyo". Anas shima ya faɗi yana riƙe dariyar dake cinsa.

"Ban sani ba dan gidanku!, ni zaku ce kamar kura ta biyo?". Mami ta faɗi tana sakin huci.

"Mami sannu da zuwa". Tijjani da duk abinda ke faruwa bai ce komai ba yayi maganar.

"Yau ɗan albarka". Ta amsa, ba tare da ta sake tanka su ba ta haye sama ta barsu suna cigaba da dariyar.

Yaran Mamin uku ne, Tijjani, shi ne babba, sai Abdulwahab, sai kuma auta Habiba da suke kira da Biba, Anas da Sadiya ƴaƴan ƙanwar mijinta ne.

Jagwab ta zauna akan katafaren gadon ɗakinta, hannunata dafe saman goshinta, abin duniya duk ya isheta, dan ba ƙaramin tada hankalinta maganar boka Darmuuje tayi ba.

Kamar wacce aka mintsina ta miƙe, ɗakin ta shiga zagayewa tana naushin hannunta, "Inaa!, hakan baza taɓa yuwuwa ba!". Ta faɗi cikin ƙaraji.

Wayarta ta jawo, number aminiyarta Hajiya Turai ta shiga aikawa kira, cikin sa'a kuwa bugu ɗaya Turan ta ɗaga kamar me jira, ko da yake dama jiran take.🌷

"Ya ake cike ne aminiya?".  Hajiya Turai ta tambaya, huci Hajiya Balaraba ta sake saki, "Ina cikin tashin hankali Turai, abubuwa na shirin kwaɓemin".

"Me kuma ya faru Hajiya?".  Ta tambaya tana dafe ƙirji, nan ta labarta mata duk yanda suka yi da boka Darmuuje, dan ta yarda da Turai ɗari bisa ɗari.

Nisawa Turai tayi kana tace "Ka da ki damu da maganar Darmuuje, kinsan suma fa wani lokacin suna faɗar abinda ba haka bane, ki kwantar da hankalinki muke da nasara, nima ina son na ɓulla gurin boka Kagalmu akan lamarin naki".

Ajiyar zuciya ta sauke a karo na biyu tace "Shi ke nan Turai, duk yanda kukai sai ki sanar dani". Da haka suka yi sallama suka ajiye wayar.

Dariya me sauti Turai ta saki bayan ta ajiye wayar,"Muje zuwa Balaraba, ai wallahi matuƙar ina raye saina rabaki da gidan Alhaji Ahmad, kamar yadda ke ma kika rabashi da tashi matar, ba ke kaɗai kika iya wasan ba".  Ta faɗi tana sake kwashewa da dariya.

Kamar yadda tace zataje gurin boka Kagalmun zata je a sake sabunta aikin dake jikin Humaida.

Dan kamar yadda ta faɗa Humaida baza ta taɓa dawowa cikin ruyuwar Ahmad ba, "Kai har abada Humaida baza ki taɓa samun lafiya bama balle ki tuna wacece ke harma ki tina kin taɓa rayuwa da wani mai suna Ahmad ba wannan alk'wari nane".

Falo ta fito zuciyarta cike da wannan alwashin.

"Mamina".  Minal dake zaune a falon tana kallon serias ta faɗi, "Na'am ƴar Mami, ya aka yi?". Tayi maganar tana zama gefen Minal ɗin, kai Minal ɗin ta ɗora akan kafaɗarta.

Kanta Mamin ta shafa, "Babyna menene?".

Hawayene suka sakko mata, ai ko nan da nan hankalin Hajiya Turai ya tashi, a rikice take tambayarta abinda ke damunta.

Cikin kukan Minal tace, "Mami T.J ne, jiya na ganshi a gurin birthday Khairy nayi masa magana yaimin banza".

"Akan wannan kike asarar hawayenki?, ki rabu dashi ya gama hayaƙin rashin mutumcinsa kamar ya aureki ya gama".

Mamin ta faɗi cikin lallashi, "Mami da gaske?". "Kwarai ma kuwa, ke dai kawai ki kwantarmin da hankalinki".
Cikin farin ciki ta rungume Mamin, "Love you more Mamina".

*NAZBEER*
🌷🌷🌷

A hankali ya kai hannunsa me ɗauke da zoben daimon da azurfa ya kunna loptop ɗin dake ajiye a saman table ɗin na shi, sai da komai ya saitu sannan ya shiga tura bayanai, wani file ne ya ja hankalinsa hakan yasa ya jawo wayar dake office ɗin ya aika kira, bugu ɗaya aka ɗaga, "Ka zo yanzu". Iya abinda ya faɗi ke nan ya katse kiran ba tare da ya jira amsar da za'a bashi ba.

Hmmm, akwai ƙura fa
To koma dai yaya ne mu haɗe daku a next page don jin yadda zata kaya.

Share and comments my lovely fans, i love you irin wujiga-wujiga ɗin nan🫶🫶🫶

*Taku*
*ABEEDAH*✍️
[5/14, 7:24 PM] Abidah: *NAZBEER*
🌷🌷🌷

*Written by*
*Zainab Laminu Sani*
(*Abeedah*)✍️

Follow this link to join my WhatsApp group:
https://chat.whatsapp.com/FP7D2LzvLM6Asy82NpHTIF

My channel 👇

Follow the NAZBEER FANS CLUB channel on WhatsApp:
https://whatsapp.com/channel/0029VbAxsXB7IUYWz4OBH713

———————————————

*FIRST CLASS WRITER'S ASSOCIATION*
(*Home of Qualites And Trusted writer's of the Nition*)☀️☀️☀️

*PAGE*----- 4

Bismillahirrahmanirrahim.

Bai fi mintina uku da kiran wayar ba, sai ga sakatariyar shi ta shigo, tayi nokin shiru ba amsa, hakan yasa ta shigo ɗin, dan tasan idan ƴan rashin mutumcin sa na kusa haka yake, yana ji za kai ta nokin yayi banza da kai ya shareka, kuma yana ganin ka ta C.C. T.V dake office d'in".

Sallama ta sake yi a karo na uku, amma bai ko ɗaga kai ba, balle ya amsa mata,
sai dai ya amsa a zuci, dan ƙasai ta baza ta barshi ya iya amsawa a fili ba, sai ka ci sa'ar gaske ne zaka ga lips ɗin shi ya motsa.

sanar da shi zuwan, Mukhtar tayi hannu kawai ya ɗaga mata, wuce wa tayi dan ta gane me ogan nata yake nufi.
"Zaka iya shiga". Ta faɗi idonta akan Mukhtar ɗin kana ta koma mazauninta ta zauna.

Sallama ɗauke a bakinsa ya shiga office ɗin na Nazbeer, ciki-ciki ya amsa sallamar, "Have a sit". Ya yi maganar kamar baya so.

Zama Mukhtar ɗin yayi yana fuskantar shi, shiru ya gifta na ƴan mintuna kafin Nazbeer ta katse shirun ta hanyar watsawa Mukhtar ɗin tambayar data rikito da kayan cikin shi, ji yayi wata gudawar na neman kufce masa.

"Ranar 4/1/2025 an fitar da kaya da sa hannunka, amma kuma a jerin docments ɗin da ka bawa company babu na wannan kayan". Yayi maganar yana tsatstsare Mukhtar da idanunsa masu rikita mara gaskiya.

Zuface ta shiga karyowa Mukhtar kamar wanda ta haɗiyi kunama, cikin in-ina ya ce, "Babb bani da masaniya akan fitar kayan sir".

Zai yi magana Tahir ya shigo, hakan yasa ya fasa maganar da yayi nufin yin, takowa Tahir yayi har gaban teburin da Nazbeer ke zaune, file ɗin daya anso daka office ɗin Khalil ya ajiye a saman teburin, "Sir daka office ɗin Khalil ne". Yayi maganar bayan ya ajiye file ɗin.

Kai kawai ya gyaɗa, "Ka kira shi Khalil ɗin". Ya faɗi cikin muryar mara hayaniya, "Ya fita yanzu, dan tare muka fito da shi ni nayo nan shi kuma ya fita".

"OKay". Ya faɗi yana mai da hankalinsa kan loptop ɗin dake gaban shi, shi ko Mukhtar zufa ta gama jiƙe shi sharaf, dan yasan shirun nan da Oga yayi ba wai ya ƙyale shi ba ne.

Har ya yunƙura da nufin magana Nazbeer ya dakatar da shi da faɗin "Zaka iya tafiya".

"Na gode Oga". Ya faɗi yana miƙewa cikin hanzari ya nufi ƙofa, da kallo ya raka bayan shi yana jijjiga kai, kafin ya saki wani mugun murmushi, irin na zan lailaya kanku a titin nan.

"Mutumina ya aka yi ne?, shigowata ke nan aka ce kana kirana, shi yasa ko office ban shiga ba nayo nan, kuma nasan wannan murmushin naka ba alkhairi bane ga wanda aka yiwa shi". Khalil dake zaune a cikin ɗaya daga cikin jerin kujerun dake jere a office ɗin ya faɗi.

Ɗan murmushin gefen baki ya saki, "Hmm". Kawai ya faɗi yana duban Kalil ɗin, "Kaya ne da zasu kai na kimanin miliyon talafin da takwas, aka fitar dasu, amma a document na company babu su".

Ido Khalil ya zaro, "Miliyon talatin da takwas!". Ya faɗi cike da mamaki, kai Nazbeer ya jinjina masa alamar tabbatarwa.

"Amma ka binciki managa kuwa?". "Shine nake ƙoƙarin yi, shi yasa nace masa ya tafi kawai".

"Ya kuma zaka ce ya tafi?". Murmushi ya sake yi kana ya ce, "Na ɗaure shi ne ta yadda bazai iya fitar da kansa ba, so nake ya kawo kansa da kansa".

Shiru ya ɗanyi, shi kaɗai yasan abinda yake saƙawa a zuciyarsa.

Nan dai suka tattauna batutuwan da suka shafi aikin nasu kafin suka fito sallah.

A hanya Nazbeer ɗin yake sanarwa Khalil fitar da zasu da yamma, "Allah ya kaimu". Da "Amin". Ya amsa suka cigaba da tafiya.

*ABIDAH*
🌷🌷🌷

A hankali take tafiya kamar me tsoron taka ƙasa, wanda bai sani ba zai ɗauka iyayi ne, haka tsarin halittarta take, sam bata da haniya ko surutu.

A ƙofar gidan nasu ta ci karo da Yaya Hashim, shima dawowarsa kenan daka gurin aikin kanikancin da yake yi.

Da murmushi ya kalle ta yace "Ƴan mata a don gari, daga ina haka da wannan yammar?". Murmushin dake ƙarawa fuskata kyau nayi, "Kai Yaya, wacece ƴan matan?".

"Gata nan a gabana, ni indai kina gabana ai bana kallon wata mace a matsayin mace, ke ka ɗai ce". Ya yi maganar idonsa akaina.

Zanyi magana na fasa, sakamakon hango Baba Habibu ya nufo inda muke yana baza babbar riga, "Kin ci gidanku, shegiyar yarinya me siffar ifritan ƙarnin farko, iskancin naki bai tsaya a iya waje ba sai kin haɗa dana gida?, to bazan lamunta ba ki lalata min yaro, sam bazata saɓu ba".

Yaya Hashim ya buɗe baki zaiyi magana Baban ya tare numfashinsa, "Kai tafi can ka bani guri, me zaka cemin akan wannan yarinyar?".

"Wallahi Baba Abida mutuniyar kirkice, sam zaton da kuke mata ba haka bane". Yayi maganar da muryar da ke nuni da ɓacin ran da zuciyarsa ke ciki.

Dan Allah ya sani baya son yaji ana danganta Abida da wata mummunar kalma.

"Ehh laillai Hashimu wuyanka yayi kauri, ni zaka duba ka cewa ƙarya nake?".

Da sauri ya ɗago kai ya dubi Baban, "Kayi haƙuri ba haka nake nufi ba".

Sosai maganganun Baba Habibu masu kama da saukar bulala a zuciyata suka shigeni, da sauri na kutsa kaina cikin gida, ina shiga na iske wani tashin hankalin duk a kaina.

🌷
Anna mahaifiyar su Baba Halliru na iske tana ta faman yin masifa, Baba Halliru duƙe a gabanta sai faman bata haƙuri yake, "Nifa Halliru na gaji da ganin yarinyar nan a gidan nan, sai kace kai ne sarkin taimako daka ganin mutane ka yayubo mana, dan haka na baka kwanaki biyu ka fitar

mana da ita daka gidan nan".

Zantuttukan Anna ke nan da suka shiga kunnena bayan na shigo cikin gidan.

"Kiyi haƙuri Anna, riƙon yarinyar nan fa tamkar jahadi ne muke yi, kuma kin san ladan masu jahadi a gurin ubangiji, tunda bazan bijirewa umarninki ba a matsayin ki na mahaifiyata, amma ina roƙon alfar guda ɗaya gurinki, ita kiyi haƙuri ki janye wannan umarnin, danko Abida amana ce me girma a gurina, bata da wata mafaka da wuce nan ɗin". Baba Halliru yayi maganar kansa a ƙasa, idanunsa na duba da suka tara ruwa.

"Allah sarki Baba, mutanen suna ƙaunata tsakaninsu da Allah". Na faɗi cikin raina, hannu na kai nayi saurin ɗauke ƙwallar data tarar min.

Take fuskar su Inna Laure dake zaune a gurin ta canza, dan ko ba hakan suka so ba.

Jikin Annan ne yayi da kalaman Baban, "Shike nan, Allah ya tayaka riƙo". Da "Amin". Ya amsa, haɗi da ƙara yi mata godiya ya miƙe da nufin fita, karo sukayi da Baba Habibu dake ƙoƙarin shigowa, sai sauri yake kamar wanda aka biyo.

"Lafiyarka kuwa Habibu?". Baba ya faɗi yana sake duban Baba Habibun, "Ban sani ba!, duk ai kai ne ka ɗaurewa yarinyar nan, shi yasa take kallon kowa a wulaƙance".

Idona na runtse cikin zuciyata ina karanto duk addu'ar data zo bakina, idon na buɗe na sauke kan Inna Hadiza dake can gefe tana sharar ƙwalla, nasan abin yafi ƙarfinta, dan ko Annar ba ƙaunarta take ba, hakan yasa su Inna Laure suka fita fada a gurin Annar, kuma ba dan bata kyautata mata ba, ita kuwa Inna Laure dama ƴar ƙanwar Annan ce, hakan yasa tafi kowa fada a gurin Annar.

Hmm akwai ƙura fa

To mu haɗe daku a next page don jin yadda zata kaya.

Likes and comments my lovely fans🫶🫶🫶

*Taku*
*Abeedah*✍️
[5/16, 12:31 PM] Abidah: Follow this link to join my WhatsApp group: https://chat.whatsapp.com/J9oI2KIySOW3LbV89O51aJ
--------------------------------------

My channel 👇

Follow the NAZBEER FANS CLUB channel on WhatsApp: https://whatsapp.com/channel/0029VbAxsXB7IUYWz4OBH713

___________________________

*NAZBEER*
🌷🌷🌷

*Written by*
(*Abeedah*)✍️

*FIRST CLASS WRITR'S ASSOCIATION*
(*Home of Qualites And Trusted writer's of the Nation)*☀️☀️☀️

*PAGE* -------- 5

Bismillahirrahmanirrahim.

*NAZMANTON*

Ɗaki ne mai duwar gaske, wanda ya kasance mallakin wasu daga cikin mutanen gidan, dan ko ba kowa ya san da shi ba daga cikin jama'ar gidan, masu shi ne kawai suka san da zamansa a cikin gida.

Abinda ya dugunzuma hankulansu, shi ne kwanakin baya ɗaya daga cikin mutanen gidan ta taɓa jin wani sirrinsu, hakan yasa yanzu suke matuƙar taka tsan-tsan da al-amuransu.

Lokacin matar tayi yunƙurin sanar da wani abinda ta gani ɗin, wannan shi ne girman kuskuren data aikata, dan ko tayi nadama, ko in cema tana kanyi, kuma zata cigaba da yi har ƙarshen rayuwarta,

Yau ta kama ladaba, wacce hausawa ke mata laƙabi da ta bawa ranar samu, hakan take ga ma'abota ɗakin duhu, domin yaune suke shirin shiga meeting domin tattaunawa akan meeting

ɗin da suka gidanar a bankadamiyar tsafinsu.

Ƙasa-ƙasa maganganun ke tashi wanda ba kowa ne hankalinsa zai kai kai ba, muryoyi ne mabambanta ke fitowa daka baku nan jama'ar dake damfare a cikin wannan ɗaki.

"Nifa gaskiya ban gane abinda Dodo Jak ya faɗi a daren jiya ba". Wata murya mara daɗin sauraro tayi maganar, taya ma zai haɗa nasararmu da wannan matar?". Nan dai kowa ya cigaba da tofa albarkacin bakinsa.

Abinda ya kawo wannan mahara kuwa shine, daren jiya ne suka sami kiran gaggawa daka gidauniyarsu ta tsafi, sun tattauna abubuwa da dama da suka sahifi ƙungiyar da cigaban tsafinsu, har ma da nasarar da suka samu a shekarar, wanda hakan nada nasaba da mutane biyu dake hannunsu.

Abinda Dodo ya faɗa daga ƙarshen tattaunawar tasu ne ya tashi hankulansu, dama duk wanda ke da alaƙa da maganar daya faɗa ɗin.

Magana ce guda uku Dodo ya faɗi, wanda duk suka ƙara tada hankulan mazauna ɗakin na sirri, wannan fa shi ake kira rana zafi inuwa ƙuna.

Su ta inama zasu fara neman yarinyar da Dodon ya ambata? daɗin daɗawa ya tabbatar musu da samun yarinyar nan shine babban nasararsu da suke dakon jiran zuwanta, abinda ke ƙara tada hankalinsu kuwa bai wuce bincinko yarinyar nan dai-dai yake da bankaɗo labulen asirin sirrinsu, dan kawota a matsayin matar Nazbeer ba abu bane me sauƙi.

Dodo ya sake tabbatar musu da lallai-lallai su tabbata sun shigo da yarinyar cikin mantion ɗin nan, wata ƙatuwar laya ya basu da cewa da zarar sun ajiye a ƙofar da ita yarinyar zata taka shike nan ba zata yi musu musu ba akan duk abinda suka saka ta, su kuma da wannan za suyi amfani gurin sadata da Dodo Jak, shi kuma ya cika musu aikinsu da ita.

Inda matsalar take shine, ina zasu ga yarinyar?, kuma a ina take?, tunda Dodon bai sanar dasu komai akan hakan ba.

🌷

Magana ta biyu da Dodon yayi ita ce ta samo mace me cindo a ƙaramin yatsanta na hagu, , nasan da yawa zasu ce meye kuma cindo?, a cikin mutane akwai wanda ubanginji ke azurtasu da yatsu shidda, wannan na shidan shi ake kira da cindo, kuma shine Dodo Jak ya umarta da su kawo.

Za'a yanko shi tare da idon macen na dama, kuma macen ta kasance me shakaru ashirin da shida da kwana takwas, sannan za'a samo namiji shima me cindon, amma shi saɓanin ita macen, shi za'a ciro na ƙafar shi na dama tare da idonsa na hagu, shi kuma me kimanin shekaru arba'in da ɗaya a duniya.

Magana ta ukun kuwa sun saba jinta dan ƙa'ida ne indai sun zauna mitin ko wani taro, to sai ya gaya masu ita.
sun sha tambayar sa me wannan kalmar ta ke nufi, baya ce masu komai akan haka ɗin, sai dai yayi dariyarsa mara dad'in ji.
yace musu shima har yanzu yaka sa gane menene ma'anar kalmar.
amma dai ya san tabbas akwai ta.
wannan maganar kuwa ba kowacce magana ba ce.
face kullum suka tashi daga taro ko mitin sai ya ce masu, "Akwai tafiyar da ba dawowa". Sun kasa gane, meta ke nufi.
kuma kamar kullum yau ma bata sake zani ba dan da suka tashi zasu fita ɗin, sai da ya sake maimaita musu ita.

Abinda ya faru ke nan a daren jiya ɗin, da ya saka su yin mitin ɗin gaggawa, sun so su zauna tun jiyan  sai hakan baiyu wuba, dan basu suka baro gurin Dodo jak ba.
sai da misalin ƙarfe 3:40 na dare. kuma sanda suka zo gida, wasu masallatan ma harsun fara kiran farko, shi yasa suna dawowa kowa fat ɗin shi ya wuce. kamar yadda suka fita ta ɓarauniyar hanya.
to yanzu ma tanan suka dawo.

shiya tunda safe ya turawa kowa saƙo ta hanyar da suke haɗuwa bayan ɗakin miti.
suna gani basu yi ƙasa a gwiwa ba suka zo dan babu wanda yake cikin kwanciyar hanli.
Da wuri ko suka hallara, saboda suna so su samu matsaya guda ɗaya.
sun ɗauki tsayin lokaci suna  tattaunawar, sun ko samo mafitar da suke gani ta dace.

Ɗaya ne daga cikin su ya kalli wani ɓangaren da ke cikin ɗakin da yake ɗauke da daskararrun mutane, dan kuwa akafe suke babu alamar rai, koda yake ina zaka yi tsammani ganin mutum mai rai anan tunda suna cikin gilas ne.

Tsaki me sauti ta ja, "Nifa banga amfanin ajiye wannan yarinyar da uwarta da Dodo Jak yasa aka yi ba".

Wani shegen kallo wanda yake zauna ne agefen ta yayi mata.

"Aiko badan wannan ɗin da uwar ta, ta ba, da kema baki mallaki abinda kika mallaka ba, kin san kuwa ajiyensu da aka yi yasa muke samun abinda bamu taɓa samu ba, tunda ko muka fara wannan harkar".

Ɗayan dake tsaye a fusace yace, "Wai me kuke yi haka ne?, shida yasa muka ajiye su ai yafi mu sanin amfaninsu, tun da mu amfanin da suke mana shine kawai su kaimu ne ga cin nasarar mu ne".

Ba tare da wani ya sake cewa komai ba suka shiga ficewa ɗaya bayan ɗaya, ruf ɗakin ya koma ya rufe bayan sun gama ficewar, kai idan ka gani ba zaka taɓa cewa da ƙofa a gurin ba, balle kayi tunanin wani zai iya shiga.

*KANO STATE*

Hajiya Balaraba.
Suna gama wayar da Hajiya Turai.
miƙewa tayi tafara rage kayan jikinta sai da ta gama cire kayan nata sannan tanufi banɗaki dan yin wanka.

Fitowa tayi bayan ta gama shirin, kai tsaye kitchen ta nufa dan ganin abinda ƴan aikin ke yi.
Karo sukaci da Autarta Baby, "Mami kizo Dady ya dawo, yana falonsa". "To Auta, gani nan".

Falon nasa ta nufa, a falon ta iske duka yaran Tijjani ne kawai baya nan, kai suka ɗago duka suka zuba akan Mamin hadi da amsa sallamar data yi.

Gurin da Dadyn ke zaune akan kujera me zaman mutum uku ta ƙarasa ta zauna a gefensa, "Sannu da zuwa". Dubanta yayi "Yauwa, sannu, ya gidan?".

"Alhamdulillah". Ta fadi tana miƙewa ta nufi ɗakinsa dake cikin wani korido, ruwan wanka ta haɗa masa kana ta fito, "Idan ka biye surutun waɗan nan baza su barka ka huta ba".

Dariya sukai gaba ɗaya kafin ya miƙe ya shiga ɗaki.

kafin yace komai, sai ga T.J ya shigo kamar an korosa yana mazurai da ido,
ya kalli in da Anas yake "Kai Nas zoka bani key ɗin da ka ɗauka a ɗakina, ya ƙarasa maganar yana ciccijewa irin na tantiran yaran nan.

Nas ɗin da yasan ya ɗauki  motar tasa yasa ya miƙe,  "Haba Bro, ganin baka shirya ba ne yasa na ɗan fita da motar".

Shi kuwa sake haɗe fuska yayi ya miƙa  masa hannu alamun ya bashi, babu musu kuwa ya miƙa masa key ɗin.

Fisgewa kawai yayi daga hannun nashi ya juya ya fita a hanzarce, bai ko bita kan su Momi dake falon ba, nisawa Dady yayi, ƙasan zuciyarsa cike da taikaicin halin T.Jn, "Bari na watsa ruwan". Bai jira cewar Momy ba ya nufi ɗakinsa.

Koda ya shiga cikin ɗakin bai iya shiga wankan ba, saboda yadda yake jin kansa na sara masa, dole ya nemi gefen gado ya zauna.
saida ya ji, kan nasa ya daina sarawar sannan ya miƙe ya shiga wankan.

Zaune ta kai a kujerar dake kusa da ita, abin duniya ya haɗe yayi mata yawa, damuwar T.J ma kaɗai ta isheta, kai har ma da sauran yaran mata gaba ɗaya.

Biba ce taja tsaki da cewa "Kai ka jiyo can dai da mugun halinka". Ta fadi cike da rashin kunya kamar ba Yayan ta ba, ita fa Allah ya gani bata shiri da T.Jn dan baya ragawa kowa in ka cire Momy.

Sadi da ke zaune gefen ta, tace "Kin ga Biba ki iya bakinki, dan kin san halinshi, wallahi kaɗan daga aikinsa ya dawo yayi miki shegen duka, a tom ni dai ba ruwana, dan tashi ma zan yi daga gurin balle ma ya gama dukan naki ya dawo kaina".

Sake jan tsaki Babir tayi, duk da tasan gaskiya ta faɗa "To ina ruwan ki?, ke dai ki je can da wahalar ki, ke kika ga zaki iya, ta faɗi  tana sake mai da kanta ga T.V da suke kallo.

Shiru Sadin tayi, dan tasan hakan ne, dan yadda ta mutu akan son Tijjani tasan ko kanta batai wa hakan, shi kuwa baima san tana yi ba, wai kunu a wani gida.

Ita kuwa Momy tana zaune tana jin duk abinda suke cewar, ta daɗe da sanin irin son da Sadi ta kewa Tijjanin, amma hakan tasan ba mai yuwuwa bane, dan zaren ba kalar yadin bane, tasan ma ko sama take cizo mahaifiyar Sadiyan ba zata taɓa bari hakan ta faru ba, saboda

tsumammiyar tsamar dake tsakaninsu, tunda da ɗin su ƙawayene ita da mahaifiyar Sadiyan, sanadiyyar wani abu daya gifta a tsakaninsu yasa sukai uwar watsi a tsakaninsu.

*Hajiya Turai*

Kwanaki  biyu da yin wayar su da Hajiya Balaraba, ba tashirya tafiya EDO
tare da ƙawarta Itoro, da yake ita Itoron ƴar can ce.

Ita ma tayi mata hanyar Boka Kalgamu ɗin, sun shirya tafiya Edo a washegari, tunda zasu bi jirgin da zai tashi ne, daga Kano zuwa Edo awashegarin.

Tun da sassafe ta tashi ta gama shirya wa saboda karsu ɓata lokaci.
Misalin 7:20am sai ga Itoro itama a shiryan ta, basu tsaya ɓata lokaci ba suka fito, a harabar gidan suka iske  drivern  da zai kai su airfort ɗin, motar suka shiga ba tare da sun tsaya jinkirin komai ba.

Shi kuwa driver mota ya bawa wuta suka fice daga cikin gidan, kai tsaye airfort ya wuce da su, koda zuwan sun sun tarar an fara kiran fasinjojin jirgin,  saboda holdaf ɗin daya riƙe su a hanya, ba dan ma sunyi zagaye ta wasu unguwannin ba, da har yanzu ma suna can basu fita daga cikin wannan ƙaddararran holdaf ɗin ba.

Babu jimawa ko jirgin ya tashi zuwa sararin subhana.

To su Hajiya Turai dake da ƴar rakiyar taki sai muce a sauka lafiya.

To meye kuma a tsakin Hajiya Balaraba da mahaifiyar Sadiya?
A she dai rikici bai ƙare ba, da alamun ma yanzu aka fara buga wasan

To dan jin yadda zata kaya mu haɗe daku a next page.

Likes and comments my lovely fans, ina yinku irin oba ɗin nan wallahi🫶🫶🫶

*Taku*
*Abeedah*✍️
[5/17, 7:15 AM] Abidah: *NAZBEER*
🌷🌷🌷

*Written by*
*ABEEDAH*✍️

Follow this link to join my WhatsApp group:
https://chat.whatsapp.com/J9oI2KIySOW3LbV89O51aJ
---------------------------------------

My channel👇
Follow the NAZBEER FANS CLUB channel on
WhatsApp: https://whatsapp.com/channel/0029VbAxsXB7IUYWz4OBH713
---------------------------------------

*FIRST CLASS WRITER'S ASSOCIATION*
(*Home of Qualites And Trusted writer's of the Nation)*☀️☀️☀️

*PAGE*------ 6

Bismillahir Rahmanir Rahim.

*FLASH BACK*

Hajiya Mardiyya mahaifiyar su Sadiya da Anas, ƙanwa ce ga Alhaji Ahmad.
kuma kawar Hajiya Balaraba ce tun ta ƙuruciya, dan kuwa unguwar su ɗaya tare suka so.

Tun suna ƴan mata Allah ya jarabci Balaraba da matsancin son Ahmad yayan ƙawarta Mardiyya, har kuma kawo yanzu da tayi aure har mijinta ya rasu soyayar Ahmad na maƙale a zuciyarta.

Hakan yasa ta tuntuɓi amiyarta ta da maganar

Aikuwa Mardiyya tayi mata alƙawarin auren Ahmad, sosai Balaraba taji daɗin maganar.

Tun daka wannan rana Mardiyya ta shiga ƙoƙarin ganin ta shiga da Balaraba ga yayanta.

Shiko Ahmad bai ma san suna yi ba, dan tuni ya riga ya miƙa zuciyarsa ga matarsa Humaida, kyakykyawar farar mace me zubin ƴan ƙasar Kalfonya, yana matuƙar sonta, kuma sosai yake tarairayarta da bata kulawa, itama tana son abinta.

Ganinfa da Mardiyya tayi hankalin yayan nata baya kannƙawarta yasa ta shiga aibata Humaida a gurin Hajiyarsu, tun Hajiya bata ɗauka har ta fara ɗaukar zancen na Mardiyya akan fa lallai tsintacciyar mage bata mage, ta ina zasu amince a auro musu macen da ba'asan asalinta ba.

Wanan yasa Hajiya ta zaunar da Ahmada ta bashi zaɓi biyu akan ya zaɓi ɗaya a ciki.

*ALHAJI AHMAD*

Zaɓin da aka ba shi ba ko wanne zaɓi bane face.
ya zaɓi ɗaya a cikin biyu, kodai ya saki matar sa ko kuma ya auri Balaraba.

Ya shiga cikin tsaka mai wuya, dan kuwa yasan ba zai iya rabuwa da Humaida ba, hakama bazai iya auren Balaraba ba.
Shi yasa ya nemi alfarmar iyayen nasu da subashi zuwa wani ɗan lokaci, zai nemi wata ya aura, amma suka ce sam basu yarda ba.

Ganin har yanzu Ahmad yaƙi amincewa da auren Balaraba yasa mahaifiyar Balaraba, wato mai ƙosai, wadda asalin sunan ta shine Talatu, sakamakon tayi Sai da ƙosai yasa ake kiran ta da mai ƙosan, ta kai Balaraba ga Bokanta, Boka Darmuuje, ai kuwa Darmuuje yayi musu alƙawarin wannan aure babu fashi, da haka hankalinsu ya kwanta.

Suko iyayen Ahmad suka birkice akan dole sai ya auri Balaraba, a cewarsu tunda a baya sun barshi ya auri zaɓinsa to yanzu dole ya auri zaɓinsu.

Ba shida tawa mafitar dayawu ce ya auri Balaraba in dai yana son zama da matar sa farin cikin sa, dole ya yiwa iyayen sa abinda suke so.

Koda yayi yiwa Humaida maganar zai ƙara aure bata wani tashi hankalinta ba, sai dai jin wacce zai aura ɗin ya tada hankalinta, dan tasan Balaraba, tunda suka zo da Mardiyya gidan.

zauma yayi yai mata baya nin da zata fashimce shi, babu yadda ta iya face ta ba shi goyan baya ya yiwa mahaifansa biyayya.

Anyi aure lafiya kuma amarya ta, tare a ɗakinta, dan kuwa bawani shagali ka aka yi ba, a cewarsu tun da ba yara bane.

Bayan sati biyu da biki suna zaman su lafiya, kafin mahaifiyarta ta sake ɗora ta akan keken ɓera, dan kuwa tunzuwan da sukai gurin Boka Darmuuje a lokacin auren Ahmad, bata sake zuwa ba.
dan kuwa ita bata shiga gidan bane dan tafitar da Humaida ba.

Amma zigar da mahaifiyar ta da ta Mardiyya yasa ta, takoma, dan kuwa a lokacin Humaida naɗauke da tsohon, kuma ganin maganarsu Mardiyya na kan hanya da suka ce da zarar Humaida ta haifi namiji, to komai na Alhaji Ahmad Humaida ce zata shi.

Kuma a lokacin Mardiyya ta tayar da tsohuwar yarjejeniyar su, abinda mutane basu sani ba shine, Balaraba da Mardiyya sunyi yarjejeniya akan idan Ahmad ya auri Balaraba to itama zata sa Yayanta Abdussalam ya auri Mardiyyan.

Idanu Balaraba ta murje tace sam bata san da wannan yarjejeniyar ba, nan fa rikici ya kacame tsakaninsu, nan fa kowa ga fahimci abinda suka ƙulla ɗin.

Duk yadda Mardiyya taso Yayan nata ya saki Balabara abin ya ci tura, dan ko Boka Darmuuje tsaye yake akan aikin dake jikin Ahmad ɗin.

Wannan lamari yasa sukai rabuwar ba daɗi, amincinsu na shekaru ya rushe.

Wannan ne dalin da yasa Momi bata ganin auren Sadiya da Tijjani zai yuwu, ko da kuwa Sadiyan zata mutu.

Bari mubi ƴan Edo

*EDO STATE*

Hajiya Turai, sun sauka a babban airfort ɗin dake birnin na Edo, wani me takzi ne ya ƙaraso

gurin da suke "Hajiya tafiya ne?".  Ya faɗi yana ƙoƙarin ɗaukar jakar Hajiya Turai dake ajiye a gefenta, "Eh".  Motar suka shiga suna tafe Itoro na yi masa kwatancen unguwar.

Tafiya suke tayi kamar zasu sake barin gari, sai da su kazo wajen wani ƙaramin ƙauye sannan naga an sake ɗaukar wata hanyar anan ma sunyi tafiya mai yawa kafin suka tsaya a gefen wani rafi.
Shiko me mota sai faman zazzaga masifa yake, dan bai san haka tafiyar take ba, da bai ɗakko su ba, suko ƙala kanzul ba su ce masa ba.

"Gaskiya Hajiya kuɗinku dubu talatin ne". Ya ƙara faɗi bayan ya dai-daita tsayuwar motar, "Dubu talatin?". Itoro ta faɗi ido waje, wacce tafiya aka yi da zasu biya har dubu talatin?.

"Kinga Itoro rabu da shi".  Hajiya Turai tayi maganar haɗi da saka hannunta a jaka ta ciro kuɗin ta miƙa masa ba tare data irga ba, baki me motar ya washe ganin kuɗin.

Ruwan suka durfafa kai tsaye ba tare da ko tsoro ba, ko da yake zuciyar tasu ta riga ta taurare, babu abin da zai basu tsoron.

Tafiya suka fara yi a cikin ruwan da yake da girma da tsayi, sun ɗauki kusan mintuna goma kafin suka isa ƙarshensa.

Ajiyar zuciya me ƙarfi suka sauke suna duban makeken daji me ɗaike da manyan bishiyu masu siffar ban tsoro  dake gaban su, su Hajiya Turai ko ajikin su, dan kuwa haka suke ta ratsa wa'in nan bishiyun.

Sun yi tafiya me ɗan tsayi kana suka isa bakin ƙaton dutsen da Boka Kagalmu ke zaune, dutse ne me girman gaske ga kuma gefen dutsen an zane shi da wasu rubutu wanda daka gani zaka gane na tsafi ne.

Mamaki ya cika Hajiya Turai ganin dutsen ya tsage hanya ta buɗe ɗoɗar, kai kace dama can da ita, ita kuwa Itoro ko ajikinta, dan wannan ba baƙon abu bane a gurinta.

*DAKWA*

Inna ce ta kama hannuna muka wuce ciki dan yin sallar magariba, shima Baba masallaci ya tafi, baidawo ba sai da a kai isha sannan ya dawo, abinci Inna ta kawo mai nima fitowa nayi na zauna akusa da su muna ci, muna hira.

Ganin tara ta kusa na yi musu sallama na shige ɗaki don gobe da makaranta, kasa bacci na yi sakamakon tarin abubuwan dake dan ƙare a zuciyata, na jima a haka kafin bacci me nauyi ya kwasheni.

Washegari da wuri na tashi na gama shirina, a tsakar gida na iske Inna tana hura wuta, "Inna ina kwana?". "Lafiya lau, har kin kama shiryawar?". "Eh, Inna yau muna da jarabawa ne, shi yasa". "To Allah ya bada sa'a". Da "Amin". Amsa, "Amma dai ba haka zaki tafi baki ci komai ba ko?". Inna ta tambaya tana cigaba da hura wutar.

"Inna bana so na makara, lokaci yana tafiya". Duk yadda naso tafiya Inna ta hanani, babu yadda na iya haka na tsaya sai da naci abincin.

Baba Halliru su biyar ne a gurin iyayensu Malam Bala da mahaifiyar Huraira wato Anna, maza uku ne, Baba Halliru, shi ne babba, sai me bi masa Baba Habibu, sai ƙannensu mata biyu,Baba Halliru sai Baba Habibu, sannan sai Baba Adamu.

Baba Habibu matansa biyu da yara biyar, Hashim ne babba sai sauran ƙannensa mata.

Baba Halliru matansa biyu, Inna Hadiza ita ce ta farko yaranta biyu, Musaddiq da Bashir, sai kuma ni data ke kira da kyautar Allah, sai Inna Salame dake da yara uku duk mata, Shamsiyya ita ce babba sai Sakina sai kuma Umma Kulsum, taso samun maza sai Allah bai nufa ba, a cewarta Inna Hadiza ce ta yi mata asiri ta haifi mata.

Sai Baba Adamu, matansa biyu, Inna Atika , yaranta biyu, Usman da Aliyu, matar babu ruwanta da shiga lamuran mutane, hakan yasa take zaune lafiya.

Wannan shine tarin gidanmu a taƙaice, ko ince gidan da ƙaddara ta mallakamin shi a matsayin namu, dan a halin yanzu bani da inda yafi nan ɗin.

Gidan su Amina na shiga, dan dama tare muke tafiya kullum, zaune na isketa tana cin abinci, "Har kin fito?". Tayi maganar tana kai abincin bakinta, zama nayi a gefenta haɗi da wurga mata hararar wasa, "Ban sani ba, kina ganin lokaci na ja, shine kika tsaya kina wani yanga". Dariya ta kwashe da ita, "A'a, Abidah kin fito?". Umman su Amina ta faɗi tana fitowa daka ɗaki.

"Ehh, Umma". "Ki zauna ku ci abincin mana". Kai nayi saurin girgizawa, "Na ƙoshi Umma".

Tafiya kaɗan muka isa makarantar tamu, kasancewar bamu da wani nisa sosai, "Wai!, Allah yaso ba muyi latti ba". Na faɗi lokacin da muka shiga harabar makarantar, dan Allah ya gani ina masifar tsoron bulala.

Aji muka nufa da ɗan sauri dan hango Malam Hafiz zai shiga ajin, sosai mukai karatu, haka ma jarabawar da mukai ina da tabbacin zan sami cin kusan kaso biyu bisa uku.

Koda aka tashi a gajiye muka yo gida, da sallama na shiga sashen namu, babu kowa da alama Inna tana ɗaki, ɗakina na shige hadi da faɗawa kan ɗan ƙaramin gadona, ajiyar zuciya na sauke dan babu ƙarya yau ɗin nan na gaji sosai.

"Har kun dawo?".  Na jiyo muryar Inna na faɗi, "Kai Inna hakan ne har?, tun fa safe muke makarantar".  Na yi maganar ina fitowa.

Kai kawai Inna ta girgiza "Allah ya shiryeki".

Mu haɗe daku a next page don jin yadda zata kaya

Likes and comments my lovely fans, ina yinku oba wallahi🫶🫶🫶

*Taku*
*Abeedah*✍️
[5/19, 8:33 AM] Abidah: *NAZBEER*
🌷🌷🌷

*Written by*
*ABEEDAH*✍️

Follow this link to join my WhatsApp group: https://chat.whatsapp.com/J9oI2KIySOW3LbV89O51aJ
---------------------------------------

My channel👇
Follow the NAZBEER FANS CLUB channel on WhatsApp: https://whatsapp.com/channel/0029VbAxsXB7IUYWz4OBH713
----------------------------------------
Follow me on telegram 👇

https://t.me/+3USo7e9asLpmNzc0
___________________________

*FIRST CLASS WRITER'S ASSOCIATION*
(*Home of Qualities And Trusted writer's of the Nation)*☀️☀️☀️

*PAGE-------- 7*

Bismillahir Rahmanir Rahim.

Da ɗan hanzarin ya fito daga office ɗin, "Sai ina kuma haka, ba kace zamu fita ba?". Khalil dake ƙoƙarin shiga office ɗin nashi yayi maganar.

Kai ya ɗan dafe, "Kaga ma har na manta da maganar fitar, kuma yanzu Abbu ke kirana da mun fitan, kana ji ko dama gurin Malam Salihu zame je ne".

"To ai sai mu bari zuwa gobe sai muje da wuri ko?". "Hakan za'a yi kawai". Wucewa ya yi, shi kuma Khalil ya shiga office.

Gad ɗinsa ne suka taso da hanzari suka buɗe masa mota, shiga suka sannan suka fita daka ma'aikatar, a bakin get ɗin mantion ɗin suka danna hon, cikin sauri masu gadin suka buɗe, dan sun san baya son jira.

Tafiya suka shiga yi a saman kwalta dake shimfiɗe a mantion ɗin, sai da suka dan gane da gurin da aka tanada domin ajiye motoci, motoci ne birjik a gurin wasu ma duk sun yi ƙura saboda an jima ba'a yi amfani dasu ba.

Motar aka buɗe masa ya fito, kai tsaye sashen da yafi ko wanne girma a cikin mantion ɗin ya nufa, cike da jarumta yake tafiyar, wanda hakan ɗabi'arsa ce.

Sassa bakwai ne a jerin gidajen dake cikin Nazmantion, sashi na farko shine sashen mahaifin Nazbeer wato Alhaji Bashir Rimi, matansa biyu, Hajiya Abida ita ce ta farko sai kuma Hajiya

Shuwa.

Hajiya Shuwa da aka kira da Mamma, ita ɗin tsohuwar matar wani ɗan majalisa ce, yaran huɗu, biyu mata, biyu maza, mazan suna gidan mahaifinsu, matan ne kawai a gurinta.

Ta aure shi ne saboda cimma wani buri nasu, dan kuwa ƙaninsa ne ya shige mata gaba gurin auren nasa.

Da farko data je gurinsa ƙin sauraronta ya yi, ganin hakan ba mafita bace yasa sukai shiri na musamman akan sa, wanda shi da kansa ya buƙaci auren nata, ba kuwa a ɗauki lokaci ba aka yi auren.

A zahiri ita ke kula da lalurar Ummi, amma a baɗini suna tufka ne tana warwarewa ba tare da kowa ya fahimci hakan ba.

Haihuwarta ɗaya da Alhaji Bashir, babu tsarin hakan a cikin burin su, dan kuwa babu tsarin haihuwa a shirin nasu, amma sai cikin ya yi musu kutse a shirin su.

Nazbeer shine ɗansu na farko, sai ƙaninsa Fahad da kuma auta Humaida wacce suke kira da Labila, kasancewar ta ci sunan ƴar uwar mahaifiyar su ne.

Yau kusan shekaru biyu ke nan Labiba tayi ɓaran dabo a gidan, anne meta ko masa ko ƙasa babu, domin kuwa ko ranar da abin ya faru, jama'a da dama sun tabbatar da ganinta ta shiga ɗakin Ummin su, amma babu wanda ya ga fitowarta, wannan lamari ya tada hankulan mafiya yawan jama'ar gidan.

Sai sashen Alahji Mutallab wanda suke kira da Abba, matansa biyu da yara shida, Hajiya Kulu da ake kira da Mama ita ce uwar gida, yaranta uku, Hafiz da Hafiza ƴan biyu, sai ƙaramarsu Ruƙayya, Allah ya ɗora mata bala'in son Nazbeer, shi kuwa bai ma san tana yi ba, ita take kiɗanta take rawarta, se kuma mahaifiyar Mama.

Dan ita ma tana da nata shirin akan auren, hakan yasa take takurawa Abba akan ya sami Abbu akan maganar auren nasu.

Sun shirya da zarar anyi auren Ruƴayyan ta sami ciki zasu kashe shi Nazbeer ɗin,dan idan ya mutu Ruƙayya ce zata gaji duk abin da ya mallaka ita da abin da ke cikinta.

Dan wannan dukiyar tasa ba ƙaramin tsaya musu a ƙahon rai ta yi ba, ita ganin Mama ta ya ita nata ɗan ba shi da ko rabin dukiyar Nazbeer ɗin, hakan yasa ta dage akan Nazbeer ɗin sai ya auri Ruƙayya.

Amma mahaifinsa yace ba zai masa tilas ba, matuƙar shi da kan shi yana son ta hakan suke so, a lokacin da ya yi wannan maganar Abba ji ya yi kamar ya shaƙe shi ya mutu kowa ya huta, dan shima akwai na shi ɓoyayyen burin akan dukiyar Nazbeer ɗin.

Dan dukiyar ta tsaya masa a rai, tun da daɗewa yake burin tara dukiya irin haka, amma abin ya ci tura, sai shi wannan yaron daya taso jiya-jiyan nan, ya tara abinda ya daɗe yana burin mallaka, yana burin samun dukiyar ko ta halin ƙa-ƙa.

Sai matarsa ta biyu Hajiya Falmata da ake cewa Dada, yaranta biyu, Faisal da Abdurrahman, su kaɗai Allah ya azurta ta dasu, bata da damuwa, mace ce me sanyin hali, hakan yasa ta iya zama da Kulu.

Sai ɓangaren Alhaji Sulaiman da ake kira da Dady, matarsa ɗaya Hajiya Sadiya wato Umman yara, dan tana son yara, hakan yasa ake kiranta da hakan, yaransu uku, Fadila da Nabila, sai auta Auwal.

Ita ma irin burin su ɗaya da Hajiya Kulu, dan tana burin Nazbeer ya auri ɗaya daga cikin yaran nata, wannan dalili yasa Ruƙayya da Nabila basa shaƙar iska guri ɗaya, dan kowacce tana dankon soyayyar Nazbeer, haka ma iyayen nasu basa jituwa sam.

Sai ƙaaramar ƙanwar su, Mubinat, tana aure ne anan Abujar, da yaran ta biyu, Farhan da Fauwar.

Sai kuwa ɓangaren me gayya me aikin
wato Nazeer Bashir Rimi wanda aka fi sani da Nazbeer, sashen duk ya fi sauran sashen girma dama duk wasu abubuwan ƙawa, dan sashen ƙarshe ne a wajan kyau, komai ya ji ba ƙarya.

Sai kuwa sauran sashen guda uku, wanda suma ƴan uwan su Alhaji Bashir ne, wanda suke uba ɗaya, mahaifin su ɗaya, uwa kowa da ta shi, dan su su Alhaji Sunusi su biyar ne a gurin mahaifiyar su.

Alhaji Tanimu shine babba, matansa uku da yara takwas, uwar gidan sa ita ce Hajiya Bara'atu, ana kiran ta da Hajiya Babba, yaran ta hud'u Buhari da Saifullahi sai kuma Fa'iza da maimuna, itama dai Faiza tana cikin jerin su Rukayyah masu dakon wahalar son wanda bai san suna yi ba.

Sai Hajiya Rakiya wadda ake kira da Ammi, yaranta uku, Yusuf da Mukhtar sai, Fatima.
Sai Hajiya Mabaruka, da take da yaro ɗaya, Al-amin.

Sai sashen Alhaji Sunusi, shima matan sa uku, da yara uku.
uwar gidan sa itace Hajiya Suwaiba, wadda ake cewa Hajiya ƙarama, kuma itace ta haifi duka yara ukun.
Munir sai Muslim da Hanifah.

Sai Hajiya wasila, wadda mijin tane yayi mata laƙani da, Umman Yaya, dan kuwa yace, ya bar mata Munir, duk da kuwa uwar sa tace bata yarda ba, amma bai bi takan zancen taba, tun da dai yaro ai nasa ne, kuma bata isa take abinda yayi niyya ba.

Sai Hajiya Nafisa, wadda ake kira da Anty Nafi.

Sai sashen uncle Usman, da yake da mata ɗaaya, mai suna Hajiya Hafsa, ana cemata Anty amarya, sai yaron su ƙaarami mai suna Annur.

Sai Kuma sauran ƙannen su mata su biyu, Hajiya Na'ima, wato Mami, wadda take zaune a gidan yanzu, saka makon auren ta ya mutu, kuma bata koma can Rimin ba, saita zauna anan saboda aikin ta.
sai autar su, mai suna Salamatu, wadda ake kira da Anty Mami,
ba'a dade da auren ta ba, kuma acan Rimi aka aje ta, tunda mijin nata kasuwan cin shi a can ya ke yi.

Wannan shine taƙaitaccen tarishin wannan Mantion ɗin, da nazauna cikin shi, halayan wasun su kuwa sai a cikin labarin zaku ji.

*NAZBEER*

Suna gama gyara fakin, aka buɗe mai ya fito, a hankali ya ziro ƙafarsa ɗaya, kafin ya fato gaba ɗayansa, katsaye sashen sa ya nufa, a hankali ya murɗa handil ɗin ƙofar ya buɗe ya shiga, "Ma sha Allah".  Na faɗi dan ganin wani katafaren falo, ya haɗu, harya gama haɗuwa, fan kuwa ya ji komai na more rayuwa, irinsa ake kira da aljannar duniya, mabuls ɗin da yake kamar ƙanƙara a shimfiɗe a falon, fara takawa yayi, ya shiga har cikin tsakiyar falon da yake ɗauke da manya-manyan kujeru, na company vento furniture,
akan doguwar kujera ya zauna, ya lumshe idonsa.

Sai da ya gama hutawa, kafin ya tashi, ya nufi sama, ƙafar benen da take a falon ya nufa,wadda ita kanta abar kallo ce,dan kuwa an yita ne da zallar gilas fari mai garai-garai kamar an zuba ruwa.

A hankali ya fara haura wa, saboda tsahon da yake da shi, saida ya gama haura wa, kafin ya danna ɗan wani maɓalli da yake ajikin bangon gilas ɗin da aka yi shi kamar dan kwalliya ya zuge kan sa gida biyu, sai ga wani haɗaɗɗen falo da ya fi, na ƙasa kyau sosai, wasu ƙofofi guda uku da suke cikin falon ya nufi guda ɗaya ya shiga.

Shi ma kansa ɗakin abin kallo ne, dan kuwa ɗauke yake da wani irin gado me matuƙar kyau, wadrop ɗin dake maƙale a bangon ɗakin na saki baki ina kallo, ganinsu na glass me kalar blue, kai komai ya ji a ɗakin.

Kayan jikinsa ya shiga ragewa da nufin shiga wanka.

*Hajiya Turai*

Tafiya suke yi a cikin dutsen dan shima wata alƙaryace a cikin shi, a ƙkfar wani kogo suka tsaya, kafin suka kai duƙe suka fara tafiya da rarrafe har suka shiga ciki, wata tsawa aka da kamasu, da wata murya mara daɗi.

Muryar Boka Kalgamu suka ji yana wata irin dariya mara daɗin ji,
kafin suka ji muryar nan da taimasu tsawa lokacin da suka shigo, dan kuwa ƙa'ida ce wannan tsawar itace zata fara yi maka marhabun lale da zuwa.

Izinin zama aka basu kuma har wannan lokacin basu ga Boka Kalgamu ba,sai da suka zauna akan wata baƙar tabarmar kaba, wadda kana gani kasan ta tsafi ce, suna zama suka ji ɗakin ya fara wata irin girgiza alamun bayyanar Boka Kalgamu ke nan.

To su Turai wannan irin tafiya haka?, ko da yake ance aikin sa kai...

To mu haɗe daku a next page dan jin yadda zata kaya.

Likes and comments my fans, ina yinku oba wallahi🫶🫶🫶

*Taku*
*Abeedah*✍️
[5/21, 3:32 PM] Abidah: *NAZBEER*
 🌷🌷🌷

*Written by*
*ABEEDAH*✍️

Follow this link to join my WhatsApp group:
https://chat.whatsapp.com/J9oI2KIySOW3LbV89O51aJ
---------------------------------------

My channel👇
Follow the NAZBEER FANS CLUB channel on WhatsApp:
https://whatsapp.com/channel/0029VbAxsXB7IUYWz4OBH713
---------------------------------------
Follow me on telegram 👇

https://t.me/+3USo7e9asLpmNzc0
________________________

*FIRST CLASS WRITER'S ASSOCIATION*
(*Home of Qualities And Trusted writer's of the Nation)*☀️☀️☀️

*PAGE--------8*

Bismillahir Rahmanir Rahim.

Ai ko sai ga shi ya bayyana, sanye cikin wasu jayen bantai da iya alaurar shi kawai ta rufe.

baƙi ne sosai me ɗauke da wata faffaɗar fuska da ƙatoton hanci da baki cike da haƙora kata-kara jawur dasu, kai daka fanin siffarasa ma sai kaji tsoro.

Cikin wata irin murya yace, "Ki ajiye abinda kika zo da shi, za'a yi aikin". Kana daga ƙarshe ya buƙaci da su samo saɓar maciji, dan kuwa kamar yadda saɓar ke fita daga jikin macijin haka Hajiya Balaraba zata fice daga gidan Alhaji Ahmad ɗin.

Duk da kuwa ita ma tana da wani hatsabibin Bokan, amma hakan bashi zai sa ya ƙi yin na shi aikin ba, duk dako da wuya, yayi tasiri ajikin nata, saboda Bokan nata, shima hatsabibin kansa ne, amma zai gwada tunda ya san zai samu kuɗi sosai a gurin Hajiya Turai.

Idan ya yi mata aikin bai yi ba, wannan matsalar tace, ba tashi ba, tunda shi dai ya dafe kuɗin sa, to can da matsalar ta, shi dai kawai amsane nashi.

Bata da haufi akan Boka Kalgaamu, dan kuwa sai dai in baka kawo aiki gurinsa ba, amma take yanke aikinsaiyake ci, a ƙaramin tunanin tafa amma, tana ganin shi kaɗai ne maganin matsalar ta, wa'iyazubillahi meyasa wasu mutanen suke mantawa da mutune, shin harsun manta da kwanciyar kabari,
me yasa, meyasa, meyasa ne wasu mutanen suka kasance masu yawan mantuwa, shin harsun manta da irin azabar da Allah subhanahu wata ala, ya tanazarwa masu yin shirka,
Allah yana iya yafe dukkan wani lefi da mutum dan Adam zai iya aikatawa koda ya kai cikin kuffar kogi, matuk'ar ya tuba, amma banda shirka, dan Allah baya taɓa yafewa wanda yai masa shirka.

Allah ya ganar da mu, hanya ta gaskiya ya kare mana imanin mu, ya hanamu neman wani abu agurin wanin sa.
Allahumma ameen.

Haka Hajiya Turai ta ajiye masa maƙudan kaɗaɗe, har dana saɓar macijin da ya buƙata, bata san inda zata same ba, hakan yasa ya yan kamata wasu kuɗadɗen akan za'a sa ɗan autan aljanu ya samo shi, shi yasa ma ta aje masa maƙudan kaɗaɗen.

Ta yi masa maganar ƴarta akan auren su da Tijjani ɗan gidan Hajiya Balaraba ke nan, karta da mu ya ce mata duka zai yi aiki akan su har shi yaron. Da kuma mahaukaciyar matan nan, duk da da ma har yanzu ma aikin da yai mata yana tare da ita bai bar jikin taba, duk kuwa da ƙoƙarin wasu mutane na ganin aikin ya bar jikin ta, amma hakan ya gagara.

Da haka dai su Hajiya Turai da Itoro, suka baro gurin Boka Kalgamu. Yanzu kam cikin gari suka nufa tare da mai tasi ɗin da suka tare bayan fitowar su daga cikin wannan dajin.

Wani ƙaramin ƙauye suka nufa me suna Bingo, shine asalin garin su Itoro, wanda neman kuɗi ne ya fito da ita zuwa jahohin arewa, kuma anan suka haɗu da Hajiya Turai, dan kuwa irin masu sai da abincin nance nakan hanya, kuma alayin gidan su Hajiya Turai ɗin take da zama, kuma anan suka haɗu, har ta yi mata hanyar gidan Boka Kalgamun, tun lokacin da za tai auren ta na farko.

A nan suka sauka kafin gobe su ɗau hanyar komawa gida.
da isarsu gidan wajen kwanciya kawai suka nema babu batun yin sallah koda yake Hajiya Turai ce kawai ya kamata ta yi irin wannan tunanin, tun da ita Itoro kiristance. Amma ita ma bata yi ba kawai kwanciyarta ta yi sai bacci.

Ba ita ta farka ba sai da rana ta fara shigar mata ido, kafin ta miƙe zumbur kamar wadda aka tsunkuna, Itoro ta tambaya yanzu k'arfe na wane?, kallon ta ta yi ta ce "Ai lokaci bai wuce ba, saura minti talatin yanzu tara da rabi ta yi". Wanka ta shiga bayan ta gama jin bayanin na Itoro.

A gurguje suka ƙarasa shiryawa kafin suka fito, me tasi ɗin da zai kai su airfort suka ɗauka, gaf ko da jidgi zai ta shi suka isa, dan haka ba ɓata lokaci suka shige sai Abuja.

Kada suka sauka sun iske direban Hajiya Turai yana jiran su, kawai shiga sukai sai gida, a farkon layi aka sauke Itoro, ita kuma aka wuce da ita can gidan ta.

Tana shiga Baby ta taso da gudu ta rungumeta da faɗin "Momy oyoyoo, momy nayi missing ɗinki". "Ni ma haka Babyna, yanzu dai bari na shiga naɗan huta, dan na gaji sosai". Ta ƙarasa maganar ta na janye Babyn daka jikinta, "Okay Momy, sai kin fito".

*ABIDA*

Bayan fitar Inna, kayana na cire na ɗaura zani na fito na shiga wanka, ina fitowa na tarar Inna har ta ajiye min abinci, shiryawa na sake yi cikin kayan islamiyyata,kalar blue.

Abincin na ɗauka na fara ci, jifa-jifa muna hira da Inna dake zaune a bakin murhu, hannu na wanko bayan na gama cin abincin na zura gijabina har ƙasa sannan na ɗauki jakata na yiwa Inna sallama na fice, ba tare dana yiwa sauran ƴan gidan magana ba, dan du ƴan ganin dama ne, sai sun gama dama suke zuwa uslamiyyar, shi yasa ma bana wahalar da kaina wajen biya musu.

Gidan su Amina na shiga ina ko zuwa na tarar ta shirya, gaisawa mukai da Mamanta dake

tsakar gidan tana tankaɗe,  da kulawa ta amsani, haɗi da  tambayar Inna, "Tana nan lafiya ƙalau".  "Ya jikin Ammin taki?".   Ta ƙara tambayata, ido na lumshe jin Mama ta taɓomin indabyake min ƙaiƙayi, dan rabonta da Ammin tun ranar bata sake zuwa ba,amma gobe in Allah ya yarda zan je nadubata, da wannan zancan zucin suka fito da ita da Amina suka wuce islamiyyar su, dan bata da nisa daga gidan su Aminar, suna zuwa ajinsu, suka wuce, dan kuwa sunyi sauka tun a watan biyun nan da ya wuce, dan kuwa  akusan ƙarshensa suka yi,  ranar 25/2/2025 suka yi saukar, yanzu sun juya hadda ne da sauran littattafan da basu ƙarasa ba.

Shiga su kai suka tarar sauran ƴan group ɗin su, duk sun zo suna shiga ajin ya ƙara hautsinewa da surutun su, dan kuwa Abida ba daka baya ba agurin surutu, amma in aka zo ɓangaren karatu, to a nan ma ƴar ba sauƙi ce, dan kuwa tana mai da hankali a karatun ta, daga na bokon har islamiyya, sai dai tafi bawa karatun addinin ta mahimmanci, dan kuwa su duka ajin antara zaƙaƙurai ne, haka suka cigaba da shirar su, har malamin su ya shigo, karatu suka fara, har sauran malaman nasu, kuma kowa ya gabatar da nasa karatun kamar yadda ya ke atsarin makarantar, ƙarfe shida na yamma suka tashi,

tare suka fito su duka group ɗin nasu, dan haka suke kullum sai dai kowacce idan aka zo layin gidan su, sai suyi sallama ta wuce, sukuma su cigaba da tafiyar su dan ko sune ƙarshen shiga gida dan ko ita sai tasauke Amina agidan su, kafin itama tawuce nasu gidan.

Da sallama  na shiga wajen mu, Inna na tarar tana alwalar sallar magariba kallona ta yi tace "Har kin dawo?". Amsa ta nayi, ina shiga cikin ɗakin kayan makarantar na cire kawai nima na fito dan yin alawar, ɗaki na shige bayan na gama, salla na kabbara na shiga ganawa da mahaliccina.

Ina idarwa kuwa na fito dan jin maganar Baba, ledar hannun shi na  karɓa ina yimai sannu da zuwa amsamin yayi da kulawa haɗi da samin albarka, wucewa ɗakin Inna Salame ya yi, dan yau a can yake, sai da yayi wanka kafin  aka shimfiɗa babbar tabarma, dan ƙa'ida ne in dai abincin dare ne to, tare ake haɗuwa aci, dan da  tare ake haɗa ma abinci da Sakina, amma uwarta ta ce baza ta yarda ba, sai dai a rabawa kowa kwanon sa.

Gudun fitina Inna ta cewa Baba a raba mana kwanon kawai, haka kuwa aka yi.

Zama nai a inda na saba zama na fara cin abincin, cikin natsuwa, Sakina na  gefena, tana latsa wayarta me madannai.

Kai kace wata waya ce babba, dan ranar da aka kawo mata Inna Salame yini ta yi tana habaice-habaice akan ƴarta tayi goshi, wasu ko a haka zasu ƙare a gida a zaune babu mashinshini, duk da Inna tasan da ni take amma bata ko ɗaga kai ta kalle taba, harta ƙaraci baƙaƙen maganganunta ta gaji.

Wayar hannunta aka kira murmushi ta saki, kafin ta ɗaga wayar, ta fara  magana ƙasa-ƙasa, dan ko ni da nake kusa da ita bana jin abinda take cewa, balle su Inna da suke can gefe ɗaya.

Dan su tare suke cin abinci da su da Baba, duk yadda Inna Salame ta so ta hana cin wannan abincin tare, hakan ya gagara, dan Baba tsayayen namiji ne a gidan sa, amma ba dan haka to da Inna Salame juya shi zata rinƙa yi.

Wayarta ta cigaba da yi cike da nishaɗi harna gama cin abinci na, bata gama wayar ba, sai ma tashi da ta yi ta shige ɗakin su, ni kuwa littattafaina na islamiyya na ɗakko.

Na fara duba karatun mu na yau, in da bangane sai naja fansul saboda karna manta inna je gobe sai na tambayi ko Amina kowasu daga cikin ƴan ajin namu.
in basu sani ba kuma sai mubari sai Malam yazo sai mutambaye shi.

Inna ce ta kira sunana a hankali "Abida". kai na ɗago na kalli Innar, "Ki ta shi kije ki kwanta dare yayi fa".   Da "To". Na amsa kana na shiga tattare kayana, a jaka na zuba na shige ɗaki ina yiwa Inna sai da safe.

Shirin kwanciya na yi haye gado sai bacci.

Yanzu fa aka fara wasan, mu haɗe daku a next page don jin yadda zata kaya.

Likes and cimments my fans, ina yin ku oba wallahi 🫶🫶🫶

*Taku*
*Abeedah*✍️
[5/22, 8:22 AM] Abidah: *NAZBEER*
🌷🌷🌷

*Written by*
*ABEEDAH*✍️

Follow this link to join my WhatsApp group:
https://chat.whatsapp.com/J9oI2KIySOW3LbV89O51aJ
---------------------------------------

My channel👇
Follow the NAZBEER FANS CLUB channel on WhatsApp:
https://whatsapp.com/channel/0029VbAxsXB7IUYWz4OBH713
---------------------------------------
Follow me on telegram 👇

https://t.me/+3USo7e9asLpmNzc0
———————————————

*FIRST CLASS WRITER'S ASSOCIATION*
(*Home of Qualities And Trusted writer's of the Nation)*☀️☀️☀️

*PAGE--------9*

Bismillahir Rahmanir Rahim.

Washegari kamar jiya Baba ne ya ta sheni da asuba, dan shi yake tashin mun da asuba ɗin, yauma tsaye ya yi a kaina har sai da yaga na tashi  na fita yin alwala kana shi kuma ya wuce masallaci, alwala naɗaura kafin na shiga ɗaki na tada sallah.

Kamar jiya ban koma bacci ba wanka nayi sannan  nayi shirin makaranta, sai da nagama shirina tsaf, kafin na ɗakko takalmi da jaka ta sai safa da hijabina, na fito gurin Inna dake zaune tana fifitamin abin karina, zama na yi ina gaida ita.

Amsa min ta yi tana miƙo min abincin da ya yi sanyi yadda zan iya ci.
godiya na yi mata na fara cin abincin a natse, safata da takalmi na saka kana na goya jakata na yiwa Inna sallama na fice.

Kamar jiya na tarar dasu duk sun shirya, ficewa mu kai daga gidan mu duka huɗun, a tare muka jera muna tafiya har makaranta, muna zuwa muka tarar za'a fara taron latti ke nan, Sakina ce ta ce "Kai Allah ya taimake mu". Dan kuwa muna zuwa a kace mu wuce, ajiyar zuciya muka shiga saukewa, da sauri muka ƙarasa shiga cikin makarantar.

Kowa ajinsu suka wuce nima dani da Sakina ajin muka wuce, muna shiga kowa ya nufi gurin zaman sa, a gurin zamana dake gaba na zauna.

Ina gama zama sai ga Malamin da muke da shi na farko ya shigo, karatu ya yi mana sosai kafin ya fita, Malamai, huɗu ne suka, ƙara shigowa bayan sa, kafin ayi birek, jakata na ɗauka na fita, zuwa nayi na siyo abinda nake so na dawo aji, ban ƙara fita ba har sai da aka ta shi, a hankalin na ke fitowa daga ajin na nufi bakin get dan a can muke haɗuwa mu wuce gida.

Tafiya muke ba wanda yake cewa komai da haka har muka kai gida sallama mu kai muna shiga cikin gidan, ido muka haɗa da Inna Laure wata muguwar harara tai min, da tasani dole na yi ƙasa da ido na, baki ta buɗe zata fara magana, na yi sauri na shige wajen mu dan na san duk abinda zai fito daga bakin ta akaina to bamai daɗi ba ne.

Inna da taganni na shigo kamar an koro ni, ta ɗaga kai ta dubeni tace "Lafiya ki ka shigo da gudu". Idona ne ya kawo ruwa, na ce mata Inna Laure ce, kai ta jijjiga tace "To ya isa, bar kukan haka, wuce kije ki cire kayan ki, kizo kici abincin sai kiyi wanka". "To". Nace mata sannan na wuce na yi duk abinda ta umarceni.

Sai da na fara cire kayana kafin na zauna na ci abincin, sannan naje na yi wanka sai da na fito na dubi Inna na ce "Inna zan je na dubo Ammita, yanzu idan na gama shiryawa". "To ma za ki gama".

Ɗaaki na shige cike da farin ciki, da hanzari na gama shiryawa na fito, "Inna na gama shiryawa zan tafi". "To a dawo lafiya ki gaida min da su, kwana biyu ban je na dubata ba, Amma in Allah ya yarda zan je na dubota a satin nan".
"To Inna zasu ji". "Sai na dawo ni". Na faɗi ina fita daga gidan.

Hanyar da zata sadani da gidan Malam na nufa, a hankali nake tafiya har na isa layin gidan Malam ɗin, wuce wasu samari dake zama a layin gidan Malam ɗin na yi, dan kullum idan zan wuce ta gurin su ina jin maganar da suke a kaina, shi yasa ma bana yadda na cika kaiwa yamma a gidan Malam, dan nasan yadda layin nan ba shida mutane sosai, dan kuwa sabuwar unguwa ce wadda kangwaye suka fi yawa, dan duk yawan cin su amfara ginawa ne ba kuma a ƙarasa ba.

Dan wa'innan samari da babu Allah a ran su tsaf zasu aikata min abinda ransu yake so.

Ɗaya ne daga cikin su ya taso zuwa inda ne, ni kuwa gabana banda faɗuwa babu abinda ya ke yi, ina ta karanta duk addu'ar da tazo min baki na, a gabana ya tsaya "Ƴammata jimana, gabana na faɗuwa na ɗago kaina na kalle shi, zai yi magana ke nan sai ga Malam a mashin ɗinsa, tsayawa ya yi, ya kalli wannan saurayin "Ya aka yi ne? ko wani abu ta yi maka ne?".

Kai ya girgiza, Malam yace "Ai na zata ko wani abu ta yi maka".
kallona ya yi yace "Hau mu tafi". Aiko da sauri na hau bayan mashin ɗin, shi kuma ya ja muka tafi, a hanya muna tafiya ya ke cemin na yi hankali da samarin nan, dan ba imani garesu ba, dan su ci zarafin mace ba komai bane a gurinsu, kuma babu wanda zai iya yi musu komai, tunda iyayensu sun ɗaure musu ƙugu.

Da haka muka ƙarasa gida, muna zuwa na sauka na shiga cikin gidan, da sallama matar sa ce Mama Maryam ta leƙo "Au dama ke ce a gidan namu yau?". Dariya nayi na ce "Eh Mama wallahi ni ce".

Murmushi ita ma ta yi tace "To ma sha Allah, ki ƙarasa ta na ciki". Shiga na yi da sallama, kamar kullum tana zaune taƙurawa waje ɗaya ido, zama na yi a kusa da ita ina kama hannun ta a cikin nawa.
*NAZBEER*

wanka yayi sannan ya fito, ɗaure da tawul a ƙugun shi, hannunsa riƙe da wani ya na tsane ruwan jikinsa.

jin wayarsa tana baburetin ya sa shi kai kallon sa kan wayar dan ganin me kiransa a irin wannan lokacin, duk da kuwa yasan ba zai wuce Khalil ko abbu ba, ai kuwa hasashen sa ya zama gaskiya dan kuwa abbu ne ke kiran wayarta sa, sai da ya ja ɗan ƙaramin tsaki tare da, dafe kansa da yake sara masa kaɗan-kaɗan.

Hannu ya kai ya ɗauki wayar da har ta tsinke, kikaran ya bi, ai ko bugu ɗaya aka ɗaga, daga can abbu ya ce "wai baka dawo gidan bane?, tun ɗazu fa kasan kai nake zaman jira, don ina so naje na kwanta amma ka barni a nan azaune ina zaman jiran ka".

A hankali kamar me tsoron magana ya furta "Gani nan zuwa". ya na ajiye wayar, mai ya shiga shafawa a lallausar fatarsa da hutu da jin daɗi ya bayyana a jiki, sai da ya gama shafe-shafen sa, kafin ya ƙarasa jikin wadrof ɗin ɗakin da tacinye bango guda, kayan bacci masu taushi kalar ruwan sararin samaniya, marasa nauyi ya ɗakko turare ya feshesu da shi, kafin ya saka, sun yi matuƙar kyau dan kuwa kaya ko ba kwalliya ya saka suba, suna amsar jikin shi sosai, silifas, ya

saka shima kalar kayan, wayarsa kawai ya ɗauka ya fita daga ɗakin.

Fita ya yi gaba ɗaya daga sashen na shi, ya nufi sashen iyayen nasa, ya ɗan yi tafiya mai ɗan nisa kafin ya isa sashen iyayen nasa dan akwai tazara me ɗan yawa a tsakanin kowanne sashe, kafin ka iske wani.

Sallama ya yi ciki-ciki, yana shiga cikin falon, Abbu ne ya amsa mai da yake zaune yana zaman jiran nasa, kujerar kusa da Abbun ya kai zaune ya na gaida shi, amsa mass ya yi ya na tambayarsa aiki, fuska ya ɗan yatsine "Abbu ba dadī". Ɗan murmushi Abbun ya yi irin nasu na manya yana cewa, "Haba dai, tun yanzu ma da babu nauyin kowa akan ka, kace haka ina ga mata da yara sun ƙaru?". Abbun ya yi maganar fuskarsa da murmushi, fuska ya ƙara haɗewa, murmushi Abbun ya sake yi, da yasan ɗan nasa baya son a nai masa maganar aure.

Ganin yadda yake sake haɗe fuska ya saka Abbun shima ya koma siriyos, magana ya fara yiwa Nazbeer ɗin, akan ciwon mahaifiyarsa, saboda sunyi magana da Malam Sani, tun da shi an gwada nashi ba'a dace ba, shine ya bada shawarar, akan kozasu jaraba zuwa gurin wani mutum da yake a ƙasar TOGO ko za'a dace.

Nisawa ya ɗan yi ya ce "Dama gobe nima nake shirin zamu je gidan nasa da ni da Khalil, amma zuwa yaushe za'a tafi ɗin?".

Abbu ya ce "Ehh, tom, Malam yace yanzu shi mutumin ya je umara ne, amma idan ya dawo zai faɗa min sai musa lokaci ɗaya daga cikin mu sai ya je tun da Malam yace ba'a zuwa da mara lafiyar sai dai wakilin shi mara lafiyar ya je, sai in abun ya yi tsananine to sai azo da shi mara lafiyar daga baya.

"Ok". Kawai yace wa Abbun tare da cewa "Allah ya dawo da shi lafiya".
"Ameen". Abbu yace, "Yanzu goben zaka je gidan Malam ɗin?". "Eh haka nake so in Allah ya yarda". "Allah ya kai mu hakamma yana da kyau ai".

Tashi ya yi ya na yiwa Abbu sai da safe "Mu tashi lafiya". Abbun yace da shi.
Hajiya shuwa da ke laɓe a jikin ƙafar bene ta yi sauri shigewa ɗakin ta, jin Abbun ya nufo saman, tana shigewa ta fara kai kawo a tsakiyar ɗakin, wata dirowa ta buɗe ta ɗakko wata ƙaramar waya, kai kace ma tawasa ce, saƙo ta tura da bai wuce kalma goma zuwa ashirin ba. saurin maida wayar ta yi a inda ta ɗakko ta.

Gefen gado ta samu ta zauna tana ƙurawa wayar hannun ta ido, kamar yadda ko wanne sakon da minti suke bugawa, to suna bugawa ne tare da zuciyar ta.

zabura ta yi dan ganin wayar hannun ta ta kawo haske alamun shigowar saƙo, da sauri ta buɗe tana fatan ganin saƙon da take zaman jira, wata nannauyar ajiyar zuciya ta sauke saboda cinkaro da saƙon da take zaman jira, da hanzari ta buɗe tana karanta abinda saƙon ya ƙunsa rubutu ne da baiwuce layi ɗaya ba.

GOBE MISALIN ƘARFE HUƊU NA YAMMA.

Abinda saƙon ya ƙunsu kenan.
shirin bacci ta fara dan yanzu kam hankalin ta ya kwanta, shiryawa ta gama yi tsaf, ta fito tana ta baza ƙamshi, ɗakin mijin nasu tawuce, dan shi haka ƙa'idar shi take, sai dai mace ta je ɗakin shi ranar kwanan ta.

To yanzu ma baraba kwanan yake ba tun da ita Ummi bata da lafiya, sai dai Hajiya shuwa, dan kuwa ita ke ta baza mulkin ta son ranta.

shiga cikn ɗakin ta yi zaune ta same shi a gefen gado ya tafe kansa, zama tayi cike da kissa ta fara masamagana dan tana so taji gaba ɗaya shirin su akan Ummin, amma bai ce mata komai ba, duk da taji haushin abinda yayi matan, amma haka tasake kashe muryar ta tace, "Yanzu ke ban ban can-canta  naji damuwar ka ba?,
idan kace damuwar Ummi da ta yara ba da muwata bace, wannan maganar tana nufin banda mashimmanci a rayuwar a halin ka ke nan?".

Labari fa yana tafiya dai-dai, ku dai cigaba da kasancewa dani domin kaiku inda muke nufin zuwa.

Mu haɗe daku a next page don jin yadda zata kaya.

Likes and comments my fans, ina yin ku oba wallahi 🫶🫶🫶

*Taku*
*Abeedah*✍️
[5/24, 10:28 AM] Abidah: *NAZBEER*
🌷🌷🌷

*Written by*
*ABEEDAH*✍️

Follow this link to join my WhatsApp group: https://chat.whatsapp.com/J9oI2KIySOW3LbV89O51aJ
---------------------------------------

My channel👇
Follow the NAZBEER FANS CLUB channel on WhatsApp: https://whatsapp.com/channel/0029VbAxsXB7IUYWz4OBH713
---------------------------------------
Follow me on telegram 👇

https://t.me/+3USo7e9asLpmNzc0

---

*FIRST CLASS WRITER'S ASSOCIATION*
(*Home of Qualities And Trusted writer's of the Nation)*☀️☀️☀️

*PAGE--------10*

Bismillahir Rahmanir Rahim.

*NAZBEER*

Sashensa ya wuce, fitilun falon ya kashe kafin ya haura saman, a can ma sai da ya kashe duka fitilun falon saman, sannan ya shiga cikin ɗakin, zaune ya kai akan sofa da take guda ɗaya a cikin ɗakin, janyo tebur ɗin da yake tsakiyar ɗakin ya yi, dogwayen ƙafafuwan sa da suke farare tas da su ya ɗora akai, loptop ɗin shi ya ɗauka da take ajiye agefen shi, ya ɗora ta akan ƙafafuwan na sa, sai ta komai na kan ta ya yi kafin ya aika da kira tahanyar video call, ta ɗan yi jin kirin shiga kasancewa ba number ƙasar ya ke kira ba, sai da har ta tsinke ba'a ɗaga ba.

Har zai sake kiran sai kuma ya rabu da shi, ai in yazo yaga kiran nashi zai biyo, dan wata ƙila baya kusa da wayar tasa ne, ko kuma yana cikin aji shi yasa ma ya rabu da shi.

Aikin shi ya cigaba da yi har zuwa ƙarfe 3 na dare, kafin ya ta shi ya ɗauro alwala ya fara nafilfilu, ya daɗe ya na kai wa ubangijin sammai da ƙassai kukan shi, dan shi ne kawai zai iya ya ye masa damuwar da ya ke ciki, ya daɗe ya na nemawa mahaifiyar sa waraka dama duk kan sauran musulmai baki ɗaya.

Sai da aka fara kiraye-kirayan sallar farko, kafin ya miƙe da yaƙinin ubangijinsa ya karɓa masa dukkanin ad'di'oinsa, saida ya yi raka'atanil fajir raka'o'i biya, da annabi Muhammad sallahu alaihi wasallam, yace sunfi duniya da abinda ke cikin ta.

Masallaci ya nufa, koda aka idar da sallah zama ya yi ya na lazimi har gari ya yi haske, sannan ya fito cikin gidan ya shiga sashen sa ya wuce, shiri ya yi cikin kayan juging jesi masu karar blue mai haske da ratsin fari a jikin su, sosai kayan suka fito da asalin ƙirarsa ta gwarzon namiji me jini a jika, ƙafarsa ya rufe cikin farin rufaffen takalmi ya dace da kayan jikin nasa, juging ɗin ya fita.

Sai wajen ƙarfe tara, sannan ya shigo gidan, kai tsaye sashen sa ya nufa, yana zuwa wanka ya shiga, a nan ma sai da ya kwashe kusan awa ɗaaya a wanka sannan ya fito.

A hankali yake shiryawa cikin natsuwar shi, sai da ya gama shiryawa cikin suit ɗin shi kalar ruwan ganye, sun yi matuƙar yi masa kyau, agogo ya ɗaura a tsintsiyar hannunsa me cike da gargasa ta kwanta luf, alamun hutu.

Jakar loptop ɗin sa ya ɗauka ya fito daga sashen nashi, kai tsaye ma'adanar motocin gidan ya nufa, da hanzari gad ɗin nasa dake zaman dakon fitowar tasa suka buɗe masa wata haɗaɗɗinyar mota ƙirar lexus ash me duhu sai walwali take.

Sauran motocin gad ɗin suka shiga, sannan suka fice daka harabar gidan, kan titi suka harba motocin suka shiga zuƙa gudu, kasancewar ma titin babu yawan kai kawo na jama'a.

Cikin ƙanƙanen lokaci suka isa company, motar aka buɗe masa ya fito, P.A ɗin sa ya zo da sauri ya karɓi jakarsa dake riƙe a hannun gad ɗin shi.

Lifta ya shiga wacce zata sada shi da office ɗin na shi, a hawan ƙarshen liftar ta buɗe masa ya fito,  cikin office ɗin na shi ya  shige, sakatariya da hanzari ta shiga gaida shi, hannun kawai ya ɗaga mata ya wuce ciki.

Ita kuwa sakatariyar ajiyar zuciya ta sauke tana mai da kallon ta akan PA, kayan hannun shi ya miƙa mata, amsa ta yi ta nufi office ɗin da kayan, ba ta same shi a ciki ba, hakan yasa ta ajiye kayan a saman teburin dake gaban kujerar sa.

Fitowa ya yi daga cikin wata ƙofa ta gilas hannun shi rik'e da wasu file kan kujerar sa ya ƙarasa ya zauna yana ajiye file ɗin da ya ɗakko akan teburin dake gabansa, loptop ɗin ya kunna ya shiga shigar da baya nan cikin file ɗin.

Aikin sa ya ke ta yi, dan so ya ke ya gama shigar da bayanan zufa ya keyi duk da kuwa A.C da take cikin office ɗin, hakan bai hana shi yin zufar ba.

Khalil ne ya shigo da Sallama a bakin shi, dan tun ɗazu ya ke a tsaye a bakin ƙofar, tsabar aiki ya ɗau zafi bai ma ji nocking da ya ke yi ba.

Shi kuwa Khlil ko da ya shigo ya ganshi yana aiki, bai yi zaton aikin ya keba, dan yasan halin wulaƙancinsa ko da ba aiki ya keba ya na jinka za kai ta nocking ya yi ban za da kai.

shi ya sa ma ya shigo kansa tsaye, kuma ya zo ya same shi yana aiki, bai juya ba sai ma ƙarasowa cikin office ɗin da ya yi, wajen da firij ya ke ya nufa, buɗewa ya yi ya ɗakko ruwa me sanyi tare da gilas cup, tsiyaya ruwan ya yi a cikin cup ɗin sannan ya isa ya ajiye a gabansa.

Tsayaqa ya yi da danna loptop ɗin da ya ke yi ya yi, hannu ya kai ya ɗauki ruwan, dan dama ya na buƙata, bismillah ya yi ya kai bakinsa, sai da ya shanye ruwan kana ya sauke ajiyar zuciya me nauyi, kallonsa ya kai kan Khalil dake zaune a kujerar gaban teburin nasa, "Malam wa ya baka izinin zama?". Ya yi maganar cikin wasa.

"Oh, da ka samu ka dawo hankalin ka ko?".  Khalil ɗin ya faɗi ya na aika masa da hararar wasa, "Ka kama kan ka fa, da a gidan mahaukata ka ganni?.

*KHALIL*

Ɗan taɓe baki ya yi yace "Kusan haka ne".
hararar ya sake jefamai kamar idon sa zai faɗo ƙasa.
shi ma taɓe bakin nasa yabyi ya ce "Kai kasanwa kanka dai".

"Wai ma me ya kawo ka?, tun da bani na nemeka ba". Nazbeer ya yi maganar ya na duban Khalil ɗin, shi ma Kalil ɗin hararar sa ya yi ya ce "Ai ni ba sai an neme niba zan zo, zan shigo duk lokacin da na ga dama, kuma na fita a lokacin da na ga dama".

"Oh,da haka ka ke taƙama ke nan ko?".
"Eh ko da yadda za ka yi dani?". Khalil ya yi maganar ya na ɗage gira, kai kawai Nazbeer ya jinjina, "Ok, daga yau duk wanda ya sake barinka ka shigo min ba da izinina ba to a bakin aikinsa".

Dariya Khalil ya kwashe da ita, "Ai sai ka yi na gani idan zaka iya wuni guda baka ganni ba, dan nasan zama da Khalil dole".

Miƙewa ya yi ya na ɗaukar filon da ke ajiye a kujerar da take guda ɗaya a office ɗin ya jefawa Khalil ɗin ya na nuna masa hanyar fita, ya na sake ɗaukar wani
da sauri Khalil ɗin ya miƙe ya fita ya na dariya.

Ƙugu kawai ya riƙe ya na hura do gon hancin sa, duk da ya san abinda Khalil ɗin ya faɗa gaskiya ne, dan ko ya na yiwa Khalil ɗin so ne irin na ƴan uwan da suka fito ciki ɗaya, dan yadda ya ke son ƙannen sa guda biyu to haka ya ke son Khalil, kuma yadda ya ke masu kyakykyawar fata da dacewa a rayuwar su hakama ya ke wa Khalil ɗin.

Dan iyayen Khalil ɗin sun taimaki mahaifiyarsa a lokacin da take cikin buƙatar taimakon, sun tallafi rayuwarta, dan kuma Momi Safiyya tamkar ƴar uwarta ta jini haka ma Dady Abubakar ya ɗauke ta tamkar ƙanwar sa, shine sanadidyar zuwan ta gidan.

Dan kuwa a wata tafiya ne da ya yi ta gaggawa zuwa Lagos dan daga gurin aikin shi ne suka tura shi.

Bayan ya gama abinda ya kai shi can ɗin a ranar da zai dawo ne, ya bige mutun a hanyar sa ta dawowa gida, da hanzari ya fito dan duba abinda ya buge ɗin, koda ya fito sai ya isake mutum kwance kamar babu rai a tare dashi, sai da ya ƙarasa ne ma ya fashimci ashe mace ce.

Ɗaukar ta ya yi da hanzari ya sakata a bayan mota, shiga ya yi ya nufi asibitin da ya ke kusa, suna zuwa aka amshe ta, aka wuce emergancy da ita.

Har zuwa safiya likitocin basu ce ma sa komai ba,  sai kusan zuwa a zahar ne babban likitan ya buƙaci ganinsa.

Gurin zama likitan ya nuna masa a office ɗin na sa, duban sa likitan ya yi bayan ya zauna, "Babu abida ke damunta, sai dai damuwar data ke ciki tana neman taɓa ƙwaƙwalwarta, amma kada ka damu in sha Allahi normal zata farka, sai dai ayi ƙoƙari a magance mata damuwar da take cikin, saboda kada abin ya wuce haka".

Kai Dady Abubakar ya jinjina yace "In allah ya yarda za ayi ƙoƙarin aga an magance mata damuwar da take cikin". "Hakan ya kamata, in sha Allah zuwa anjima za'a iya sallamarta, tun da ba wata matsala".   Likitan ya faɗi, hannu ya miƙa masa su kai misabiha kana ya fito daka office ɗin likitan.

Kujerar dake kusa da shi ya zauna, ya nisa cikin tunanin matar nan wayar sa ta yi ƙara, cirota ya yi daga aljihu, Momy Safiyya ce, hakan ya sa ya amsa muryasa ɗauke da damuwa, dan shi mutum ne me tausayi,"Fatan dai lafiya?, tun jiya muke tammatar ka amma shiru?".  Momy Safiyya ta faɗi bayan da suka gama gaisawa,

Nisawa ya yi, "Ina asibiti yanzu".  Ya yi maganar muryarsa na bayyana damuwar da yake ciki, "Subhanallah, kai ne baka da lafiyar?".  Momy Safiyya ta tambaya cikin damuwa, nan ya labarta mata duk abinda ya faru.

"Ayya, Allah ya bata lafiya". Da "Amin". Ya amsa ya ajiye wayar da yi mata alƙawarin zarar an sallameta zai kamo hanya.

Ya na gurin zaune wata Nuse ta zo ta kira akan ya zo matar nan ta farka, a ha zarce ya miƙe ya bi bayan  nuse ɗin.

A zaune take ta juyawa ƙofar baya, ɗago fuska ta yi ta dube su bayan sun shigo, kallon rashin sani take binsu da shi, shikuwa sannu ya yi mata kafin ya ɗora da bata haƙuri akan abinda ya faru, abinda ya ɗaure masa kai shine gar yanzu kallonsa take yi.

A hankali cikin muryar masa lafiya ta fara magana, "Nan ina ne?". Ta yi maganar cikin harshen turanci, hakan ya tabbatar masa da ba yƴar ƙasar nan ba ce.

"Baiwar Allah ke ɗin ƴar ina ce?, dan nan Nigeria ce".  Ya yi maganar ta na ƙura mata ido, ya na son gane ƴar wacce ƙasa ce, hawaye ne suka gangaro mata, cikin hawayen ta ce, "Kalponoya". Ido ya fiddo waje jin daga ƙasar Kalponiya ta fito, "Ke kuwa baiwar Allah me ya kawo ki Nigeria?". Ya sake tambaya cikin turanci yanda zata fahimce shi, "Ƙaddara".  Bakinta ya faɗi.

Tofa kun fahimci wacece wannan baiwar Allahn kuwa?.
To mu haɗe daku a next page don jin yadda zata kaya.

Likes and comments my fans, ina yinku oba wallahi🫶🫶🫶

*Taku*
*Abeedah*✍️
[5/25, 8:23 PM] Abidah: *NAZBEER*
🌷🌷🌷

*Written by*
*ABEEDAH*✍️

Follow this link to join my WhatsApp group: https://chat.whatsapp.com/J9oI2KIySOW3LbV89O51aJ

---------------------------------------

My channel👇
Follow the NAZBEER FANS CLUB channel on WhatsApp: https://whatsapp.com/channel/0029VbAxsXB7IUYWz4OBH713
---------------------------------------
Follow me on telegram 👇

https://t.me/+3USo7e9asLpmNzc0
—————————————————

*FIRST CLASS WRITER'S ASSOCIATION*
(*Home of Qualities And Trusted writer's of the Nation)*☀️☀️☀️

*PAGE-------- 11*

Bismillahir Rahmanir Rahim.

Nisawa Dady Abubakar ya yi ya ce, "Amma in ba damuwa zanso na ji labarin ki, in har kin yarda da ni, kuma in Allah ya yarda zan taimake ki".

Kai ta jinjina masa ta ce "Na yarda da kai, kuma zan baka labarina, kamar yadda ka buƙata". "Alhamdulillah, zamu je gidana inda an sallameki daga nan, in yaso kya bani a can".

Murmushi kawai ta yi da faɗin "Ba komai". Tashi ya yi ya fita dan ya samo mata abinda za ta ci, bai jimaba ya shigo hannunsa riƙe da leda, Nuse ya kira dan ta taimaka masa ta bata abincin, sai da ta gama ci kana Nuse ɗin ta bata magungunanta, zuwa can wajen ƙarfe huɗu sai ga saƙon sallamarta daka gurin babban likitan.

Nuse ɗin ɗazu ce ta sake taimaka mata ta shirya,  inda Dady Abubakar yake jiran su suka fito, har wajen mota taraka ta bata sauran magungunan ta, godiya Dadyn ya yi mata, kafin ta shiga gaban motar tasa ya ja suka bar asibitin.

Kai tsaye hanyar Abuja ya ɗauka duk da yamma ta yi, dama ya ƙudure a ransa  komai dare yau a gida zai kwana in har sun sallameta, kuma tun da an basu sallamar, me zai tsaya yi?.

Tafiya suke yi babu mai cewa kowa komai, dan akwance take cikin kujera idon ta alumshe, dan ba bacci take ba kawai dai tazaɓi yin shirunne, dan bata da abin cewa. Shikuwa tuƙinsa kawai

ya ke yi, dan yana so su isa gida akan lokaci, baya son ya sake kwana ako'ina inba a gidan sa ba, shi yasa ya ke ta sharara uban gudu kamar wanda zai tashi sama. Basu suka isa gida ba sai biyar na asuba.

Suna zuwa ya danna hon mai gadi da yake alwalar sallar asuba, da ɗan gudun sa ya taso ya buɗe get ɗin, ya na yiwa me gidan nasa barka da zuwa, hannu kawai ya iya ɗaga mai, ya ƙarasa shiga cikin gidan, fakin ya gyara kafin ya kalli in da take kwance tana bacci, dan gukan gefen kujerar da take kai yayi, ido ta buɗe a hankali tana bin gidan da kallo, "Nan kuma ƙaddara ya sake shillo dani". Ta faɗi a ƙasan ranta.

Muryar shi ta ji ya na sake yi mata magana kallon ta tamayar kansa, ya sake ce mata "Ki fito mu shiga ciki sai ki kwanta ki huta". A hankali na ziro ƙafata waje kafin na fito gaba ɗaya, gidan na dinga bi da kallo, "Muje ko?".   Bayan nasa na bi har muka isa wani haɗaɗɗen falon gidan, ɗaki ya nuna min guda ɗaya daga cikin ɗakun nan da suke a falon.

Wucewa na yi ɗakin da ya nuna min na murɗa handil ɗin ƙofar sai ga shi ya buɗe, ɗaki ne babba kamar na wata matar auren, ya ji komai na more rayuwa, ƙofar da nake tunanin bayi ne na nufa, dan yin alwala, cikin sa'a kuwa na tarar bayin ne.

Daddumar dake shimfiɗe na nufa haɗi da ɗaukar dogon hijabin dake kai na kabarta sallah.

Kwanciya na yi bayan na idar da sallar, dan na gaji sosai, kuma ina buƙatar yin nazari, na rasa ahalina da dangina baki ɗaya, anya na cancanta na cigaba da rayuwa?, duk an kashe min sauran ƴan uwana, to nima me ya rage min?, "Baki san abinda Allah ya ajiye a rayuwar taki ba". Wani sashe na zuciyata ya tunasar dani.

 A haka bacci ya ɗauketa tana wannan tunane-tunanen, sai wajen azahar na ji kamar ana tashina, a hankali na buɗe idona na sauke akan wata kyakykyawar farar mata, murmushi ta sakarmin, "Ki tashi ki yi salla, sai ki ci abinci".

Tashin kuwa na yi  na shiga bayi, saida na fara watsa ruwa kafin na ɗaura alwalar na fito, sallar na yi ina idarwa sai ga matar nan "Yauwa kin idar kenan?,to ki fito kici abinci".

Bayan matar na bi har zuwa falon da muka shigo jiya, kan dining muka wuce a can muka sami Dady Abubakar, gaida shi na yi,  amsa min ya yi ya na tambaya ta gajiyar hanya, ɗan murmushi

kawai na yi,"Gajiya kam tabi lafiya".   "Ma sha Allah".

Zama nayi aka fara cin abincin, har muka gama ba wanda ya yi magana. Tashi su kai daga kan dining ɗin suka koma cikin falon, zama sukayi a cikin kujerun da suke cikin falon, kafin ya kalle ta  "Wannan mata tace sunan ta Safiyya, yau satin mu biyu da aure ke nan, ina so ki ɗauke ta kamar ƴar uwarki, duk abinda ki ke so idan ba za ki iya yimin magana ba, to ki yi mata magana zata faɗa min, ni kuwa in Allah ya yarda indai baifi ƙarfina ba zan yi maki shi".

Kallon sa ya mayar akan Momy Safiyya "Safiyya na san baki da damuwa, ina so ke ma ki ɗauke ta tamkar ƴar uwarki".

Murmushi ta yi ta ce "Ba komai in Allah ya yarda zamu zauna lafiya kalau kamar Yaya da ƙanwa".   Murmushi shima ya yi ya na maida kallon sa akan ta ya ce "Muna sauraron ki, ina so ki ba mu labarin ki, da sunan ki dama inda kika fito?".

Nisawa ta yi  "Kamar yadda na faɗa maka ni ƴar a salin ƙasar kalponiya ce, mu uku iyayen mu suka haifa".   Haka ta cigaba da bashi labarin tana hawaye har inda ƴan fashin nan suka tashi garin su da kashema ƴan uwan ta guda biyu da mahaifan su, sannan tace masu ita sunan ta Abida.

Sun tausaya ma ƙwarai, kuma suka yi alƙawarin maye mata gurbin ƴan uwan ta da tarasa, in har suna raye baza ta taɓa kukan rashin iyayen ta da ƴan uwan ta ba, godiya ta yi masu sosai godiyar da
baki bazai iya misaltawa ba, sai da Momy Safiyya tazo ta ɗaga ni daga durƙuson da na yi ta kalle ta ce "Haba ƴar uwarta, ashe baki yarda munza ɗaya ba?, tunda har kike mana irin wannan godiyar".  Kai ta jinjina masu ta ce "Anty Safiyya godiya ai tazama dole". Kai Momy Safiyya ta girgiza ta ce "A'a sai dai in baki ɗauke mu a matsayin ƴan uwan ki ba".

Dady Abubakar ya ce "Gaskiya Safiyya take gaya, saidai in baki yarda da muba a matsayin ƴan uwan na ki bane".

Hawayan idon ta ta goge  "Ba haka bane...".
Momi Safiyya ta katsema hanzari "To yane?". kai ta girgiza tace "Ba komai Allah ubangiji ya bani koda ƙanƙanuwar hanya ce da zan iya saka alkhairi da alkhairin da kukai min".  Dariya suka yi su duka suka ce "Amin".

Fita ya yi zuwa gurin aikin shi, su kuma suka yi zaman su tare a gidan kamar dama sunsan

juna, dan Momy Safiyya tana da saurin sabo, ita kuma Abidar bata da damuwa dan tasaki jikin ta da Momy Safiyyan, haka kuma sukaci gaba da zaman su babu wata matsala, amma ance zomu zauna zomu saɓa shine zama, to sumadai suna samun saɓanin, dan harshen da haƙori ma suna saɓawa,
to suma koda saɓani ya shigo tsakanin su, suna ƙoƙarin ganin ɗayan su ya danne zuciyar sa, domin suga sun zauna lafiya.

Wata rana sun ta shi Momy Safiyyan ba lafiya hakan ne yasa suka nufi asibiti cikin gaggawa, suna zuwa aka amshe ta aka shiga da ita, su nan tsaye cikin jimami sai ga wata likita ta fito tana murmushi ta kalle su "Kai ne mijin ta?". Ta yi maganar ta na kallon Dady, jiki na rawa ya ce "Eh, nine me ya faru?". Ya faɗi a ɗan rikice, dan baya fatan ace wani abun ya sami Safiyya, hannu ta miƙa mai "Fara bani goron albishir".

Aljihun sa ya shafa ya ji ba komai a ciki, fahimtar hakan da likitan ta yi, tace "Na biyoka bashi, madam nada juna biyu".

kwatanta maku irin farin cikin da muka shiga ma ɓata lokaci ne, dan ko na yi wa Momy Safiyya murnar wannan rabon da Allah ya bata, dan tana tsananin son haihuwa sai yanzu Allah ya kawo mata nata rabon.

Sallamar mu a kai muka koma gida jikin nata da sauƙi, mun cigaba da rainon cikin Momy Safiyya cike da kulawa dan ko bana barin ta, tana yin komai a gidan, ni nake yin komai.

Kuma a wannan lokacin aminin Dady Abubakar wato Alhaji Bashir ya kawo ziyara gidan, dan daga gurin aikin shi yake dan andawo da shi nan Abuja shima, ya ɗan jima a nan kafin ya yi mana sallama, suka fita shi da Dady da zai mai rakiya zuwa wajen motar sa, har gurin motar tasa suka ƙarasa Dady Abubakar ne ya kalle shi yace "Na ga tun da muka fito kake so ka yi magana amma ka kasa cewa komai da matsala ne?".

Ajiyar zuciya Alhaji Bashir ya sauke ya ce "Yarinyar da na gani a cikin ƙanwar matar kace?".

Dadi Abubakar "Wai Abida kake nufi?". Alhaji Bashir yace "Eh to ita ɗin ce". Kai Dady ya gargiza yace "A'a ba ƙanwar tace ba". Nan ya labartawa Alhaji Bashir yadda ya tsinci Abidah, sosai Bashir ya tausaya mata.

"Yarinyar ta yi min, kuma da gaske ina son aurenta". Alhaji Bashir ɗin ya faɗi ya na duban Dady.

Dady Abubakar ne yace "In ko haka ne zan baka aurenta, matuƙar ta amince, amma bana so ka dubi tarihinta wata rana ka goranta mata". Kai ya jinjina "In sha Allah ba zan baka kunya ba abokina". Da wannan suka ƙarasa gurin da motar Alhaji Bashir ke fake.

"Na san inda Abidah ce ba zata bamu kunya ba". Dady ya yi maganar lokacin da suka isa gurin motar.

Ko da ya koma gida zuciyarsa kullum cikin tunanin Abidah take, ya kasa samun sukuni, domin kuwa sonta ke nuƙurƙusar jiki da ɓargonsa.

Sai da aka sami kusan kwanaki kana Dady ya tunkari Abidah da batun Alhaji Bashir, "Ba zan tilas ta ki ba, matuƙar bakya son shi to kada ki ji komai ki sanar dani, ni kuma zan sanar da shi yanda zai fahimta". Dady ya faɗi ya na dubana.

Momy Safiyya ce ta dafa kafaɗata, "Kin gai idan har bakya son shi to kada ku cuci kanki, amma wallahi Alhaji Bashir mutumin kirki ne, domin idan haka ta faru ina tabbatar miki ba zaki taɓa yin kuka da aurensa ba, ki tsaya ki yi nazari".

Nisawa na yi "Anty tunda har kin ce haka to nima na amince, Allah ya sa shine alkhairi".
"Amin". Suka haɗa baki gurin faɗi.

Bayan kwana biyu da maganar Dady ya sanar da amininsa Alhaji Bashir, yadda su kayi da Abidah, ai kuwa ya yi farin ciki, dan ji ya yi kamar ya yi tsuntsu ya ganshi a gaban Jadda ya sanar mata a zo a nema masa auren Abidah.

"In sha Allah a satin nan zan shigo garin". Ta faɗi cikin murnar data kasa ɓoyuwa a muryarsa.

"Kai mutumina, irin wannan murna haka, kamar wanda aka cewa an ɗaura?". Faɗin Dady ya na dariya, "Ba zaka gane ba ne, bakan san yadda son yarinya nan ya gama kassarani ba ne".

Da wannan suka ajiye wayar kowa na cikin farin ciki.

*BAYAN SATI UKU*

A wannan sati ukun abubuwa da yawa sun faru, daga ciki kuwa har da sa ranar aure na da Alhaji Bashir, da kuma haihuwar  Momi Safiyya, dan a daren na jiya ne Momi Safiyyan ta tashi da naƙuda, asibiti muka nufa duk da dare ya yi amma mun sami wasu likitocin sune ma suka shiga da Momi Safiyya lebo room, da take a cikin mawuyacin hali, kafin babban likitan da Dady Abubakar ya kira tun a hanyar mu ta zuwa ya ƙaraso, ba'a jima da shiga da ita sai ga shi ya shigo, hannu ya bawa Dadyn suka yi misabiha kafin ya ce "Tana ina?".  Dadyn ne yace "Sun shiga da ita cikin lebo room ɗin".

Bai sake cewa Dadgn komai ba ya shiga cikin ɗakin da take ciki, bai fi wasu mintina da shiga ba, sai suka jiyo kukan jariri, kallon juna suka yi ita da Dady Abubakar kafin su sauke ajiyar zuciya, suna godiya ga Allah, dan ni har hawayen dadi na yi, dan dai yau ga jinin Anty Safiyya a duniya "Alhamdulillahi".  Na faɗa dan kuwa shine a bin godiya.

Nuse ce ta fito ɗauke da jariri a hannun ta, har rige-rigen amsar jaririn suke da yake hannun Nuse ɗin, Dady ne ya fara amsar jaririn yana kallon yarinyar ya na murmushi.

Abida ce tamatso "Dady mace ce?".  Kai ya ɗaga mata "An sami ƴa mace".  Ya  faɗa ya na miƙo mata yarinyar, amsar ta ta yi ta na kallon yarinyar cike da so da ƙauna, dan a kallon farko da ta yiwa yarinyar taji Allah ya ɗora mata ƙaunar yarinyar, ko da yake irin soyayyar da iyayen ta suka nuna mata, ai zata ji fiye da haka ma akan jinin su.

Izinin shiga aka bamu, shigar kuwa mu kayi muka same ta akan gadon asibitin a zaune ta na kallon kyautar da allah ya bata, ɗago kanta ta yi ta na kallon su kafin ta sakar masu murmushi, saurin ƙarasawa na yi inda take zaune, nima zama nayi a gefen ta muna kallon yarinyar tare, Dady ne ya ce "Oh! wato kun samu ƴar ku ni kuma an manta dani ko?".

Dariya suka yi duka kafin Anty Safiyya tace "Haba dai har na isa na manta da kai, kafin na ganta wana gani?".  Dariyar shima ya yi ya ce "To na sani ko har an manta da ni".  Kai ta girgiza mai tace "Ina zan iya mantawa da kai". Kafin ya sake yin magana tace "Wai dan Allah yau she zasu sallame ni?, dan wallahi na gaji da zaman asibitin nan, kawai kasa su sallame ni, na koma gida".

Dafata na yi na ce "Haba dai Anty Safiyya ki bari ki ƙara jin sauƙi mana, ko zuwa gobe sai a sallame ki".  Fur Momy ta ƙi.

Sallamar ta ta aka yi muka koma gida, kuma tun da safiyar yau muka fara  amsar baƙi, dan

Dady tun daren ya fara kiran ƴan uwan sa da na ita Momy Safiyya, shiya ma yau tun safe ƴan barka suka fara zuwa har ma da wasu daga cikin dangin Momy Safiyyan, haka kullum muke amsar ƴan barka har ranar suna, ranar suna yarinya taci suna Maryam suna ce mata Sanah dan taci sunan mahaifiyar Momy Safiyya shi yasa ma suke mata lakani da hakan.

Bayan sunan Momy Safiyya da wata uku aka yi bikina da Alhaji Bashir, anyi biki mu lafiya su Momy Safiyya sune iyayen biki dan kuwa ta zage tayi biki irin na nu nawa sa'a.

Shi ma hakan take a gurin Dady Abubakar, dan kuwa ya nuna bajinta sosai, dan duk abinda uba ya kewa ƴarsa to Dady Abubakar ya yi min, dan har kayan ɗaki da na kitchen da Alhaji Bashir ɗin ya ce ba sai ya yi ba, amma bai saurare shi ba dan kuwa ya yi min kayan da ko wata ƴar mai kuɗin sai haka, dan ko nasa ni koda iyayena ne iya abinda zasu min kenan.

Dan kuwa wa'in nan bayin Allah sun maye min dukkan wata kewa ta iyaye sun hana ni na yi kukan maraici, bani da wani abinda zan iya biyan su dabshi face nai tai masu addu'a har ƙarshen rayuwar ta.

Allah sarki Ummi, to ko ya yata kaya?, mu haɗe daku a next page.

Likes and comments my fans, ina yin ku oba wallahi🫶🫶🫶.

*Taku*
*Abeedah*✍️
[5/26, 11:51 AM] Abidah: *NAZBEER*
🌷🌷🌷

*Written by*
*ABEEDAH*✍️

Follow this link to join my WhatsApp group: https://chat.whatsapp.com/J9oI2KIySOW3LbV89O51aJ

----------------------------------------

My channel👇
Follow the NAZBEER FANS CLUB channel on WhatsApp:
https://whatsapp.com/channel/0029VbAxsXB7IUYWz4OBH713
----------------------------------------
Follow me on telegram 👇

https://t.me/+3USo7e9asLpmNzc0
____________________________

*FIRST CLASS WRITER'S ASSOCIATION*
(*Home of Qualities And Trusted writer's of the Nation)*☀️☀️☀️

*PAGE--------12*

Bismillahir Rahmanir Rahim.

Na tare anan gidan shi da yake Abuja, gida ne me kyau da tsari,dan kuwa ko makaho ya laluba yasan an narka dukiya gurin gina shi.

Ƙalubalen farko da na fara samu da a halin shi, dan kuwa ƴan uwan sa sunce sai dai ya dawo da ni nan Kano cikin nasu matan, dan bafin suna na yi ba da za'a ce ni a can zan zauna, sai da mahaifin su ya tsawatar akan hakan, sannan yace wa ita mahaifiyar su Alhaji Sunusin dan ita tace da sauran yaran ta sukace basu yarda ba, ya aje ta a can ba sai dai ta dawo cikin su, dan ita mahaifiyar tasu abinda yasa tace haka don tana ganin yaran ta ne manya agidan amma, a ce sai abin da yaran Jadda suka ga dama ake yi a gidan dan sune suke riƙe da gidan.

Balle ma shi Alhaji Bashir ɗin tunda ko a cikin yaran nata ya fi dukan su hali, dan kusan ma shi ke ɗaukar ɗawainiyar ta harma data yaran matan, kai harma da ta mazan, dan kuwa ba wata sana'a suke ba.

Amma da yake ɗan Adam mai manta alkhairi ne,  shi ne fa bayan bikin da ya ce shi a can ya ke so ya zauna saboda aikin shi kar hankalin shi ya rabu gida biyu, amma su Alhaji Sunusin su kace basu yadda ba kuma mahaifiyar su ta goya masu baya. Sai da Alhaji Babba ya rufe ido yaci mutumcinsu kana suka bar zancen.

*BAYAN WATA TAKWAS*

A wa'in nan watanin takwas ɗin abubuwa da yawa sun faru, na fari ciki harma da na baƙin ciki, daga cikin abin farin cikin da yasa meni, shine har da ƙaruwar da Allah ya bani, dan kuwa a watan da ya wuce, mu ka je asibiti dan zazzaɓin da ya sakoni gaba, gashi duk abin da na ci ko na sha to ba zan taɓa zama lafiya ba har sai na amayar da shi, amma in ba haka ba to ba zaman lafiya.

Ganin da Alhaji Bashir ya yi abin ya ƙi ci ya ƙi cinyowa, yasa ni a gaba muka tafi asibitin.

Gwajin farko suka gane ina da shigar ciki, har na sati biyu. Tabbas duk kan wani masoyina ya taya ni murnar wannan rabon da Allah ya bani.

Ban ƙara tabbatar da irin son da Momy Safiyya ta ke min ba sai da na samu wannan cikin, dan kulawa ta daban take bani, kullum ne saibta yi min abin ƙwalama taka womin, kama daga tuwon madara da gillisuwa da tuwon fulanto, kai harma da dagin su aya da gyaɗ, dama duk kan abinda tasan mai ciki tana so.

Gaskiya na ga tsantsar soyayya a gurin wa'in nan bayin Allah. Tare da su muka cigaba da rainon cikin jikina da taltali da kulawa, har Allah ya kawo haihuwa dan kuwa a ranar wata litinin na tashi da matsanan cin ciwon mara, Momy Safiyya da Alhaji Bashir ya kira ta tun lokacin da na fara jin alamun ciwon, ce ta iso tare da duk abin da ake buƙata ga mai haihuwa.

Dai-dai isowar ta faya ta fashe min. Da hanzari ta ƙaraso in da nake duƙe a kan gwiwowina na haɗa uban zufa kamar wadda ta haɗiyi kunama, koda yake ni harma gara haɗiyar kunamar a gurina, a kan abin da nake ji.

Riƙeni ta yi ta na min sannu, to ni ko jintama ba na yi saboda azabar da nake ji, zufar tashiga share min, amma da tashare da wata ta fito, wani irin nishi na saki ina sake rirriƙe Momy Safiyya, kai na take shafawa zuwa gadon bayana, tana ce min ki daure da haka kowa ya ke farawa.

Sake riƙe ta na yi ina sakin wani nishin, sai ga kai ya fara fitowa, "Kin kusa daure dai, tunda kai ya fito". Ina bana ma jin abin da take cewa, Alhaji Bashir ne yace "Hajiya Safiyya ko asibiti zamu tafi ne tun da dai abin ya gagara agidan".

Kai ta ɗaga mai ta ce "To hakamma ya yi, bari na shirya kayan da zamu buƙata". Fita ya yi ya

na jiran fitowar ta su.

Ƙaƙƙarfan nishin da na saki ne ya da katar da Momy Safiyya daga yunƙurin saki na da tayi, sake riƙeni ta yi, "Yanzu zamu tafi asibi...". Kukan jaririn da Momy Safiyya taji ya hana ta ƙarasa maganar da ke bakin ta, da sauri ta kai kallon ta kan jaririn da yake ta tsala kuka.

Da hanzari ta isa kan jaririn tasa hannu ta ɗauke shi tana nufar inda ta ajiye sabuwar rezar da tazo da ita, sai da ta yanke masa cibiya kafin ta dawo gurin da nake zaune ina mai da nunshi.

Sannu ta sake yi min tana kama ni zuwa banɗakin da yake cikin ɗakin, shi kuwu Alhaji Bashir da ya gaji da jiransu agurin mota, sai ya kashe motar ya fito, cikin gidan ya shiga a bakin ƙofar ya tsaya yace "Hajiya Safiyya lafiya naji ku shiru?". Ƙofar ta buɗe ta na dariya tace "Oh!, wallahi ni harna manta ma da mun bar ka kana jiran mu, kasan na ga sabon ango shi yasa ma na manta da kowa".

Kallon ta ya yi da sauri yace "Hajiya Safiyya ta haihu ne?". murmushi tasake yi tace "Allah ya sauke ta lafiya, an samu ɗa namiji". Hamdala ya shiga yi yana sake yiwa Allah godiya da kyautar da ya ba shi.

Nan fa ya shiga kiran ƴan uwa da abokan arziƙi ya na sanar musu, har su Jadda sai da ya kira ya sanar musu suma.

Sai da Momy Safiyya ta shirya mu tsaf ni da jaririn kana ta huta.

Jadda ta zo tare da Autar ta Mubinat, tare su ka cigaba da kula da ni da Jaddan da Momy Safiyya, wata kulawa Jadda take bani ta daban.

Ranar suna yaro ya ci suna Muhammad Nazeer, an yi shagulgula sosai, an yi ɓarin nera, kamar ba'a san zafin nema ba, na samu kyaututtuka daga abokan arziƙi, wasu ma ban san su ba.

Taro ya ta shi lafiya kowa ya watse an bar amaryar jego da jaririnta, shiryawa mukai muka bi Jadda Kano, dan ta ce ba zata barni anan ba babu me kula, babu yadda Alhaji Bashir ya iya haka ya haƙura muka tafi.

Na samu tarba me kyau daga dangin Jaddan har ma da Baban su, ga ɓangaren Hajjo da yaranta babu wanda ya taɓa zuwa da niyyar duba ni da jariri,

Sai kuma ga shi ta zo ta na mitar ban je sashenta na gaisheta ba, Jadda ce ta yi mata tatass, kana ta bar maganar.

Ita kuwa Hajjo kiran Na'ima autar ta ta yi ta tsara mata ƙarya da gaskiya, wai su Jadda sun ci mata mutumci akan matar Bashir, "Yanzu Jaddan ce duk ta yi miki haka?". Faɗin Na'imar, "Eh". "Shi ke nan Hajjo yanzu zan zo gidan". "Sai kin ƙaraso to".

Na'ima ta na zuwa suka nufi sashen Jadda, Abidah na zaune ta na shayar da yaronta wanda ya yi wayo sosai ma sha Allah da shi.

Babu ko sallama suka shigo falon kamar wanda aka jefo, kallon su ta ta yi ta watsar, dan ita bata ma san Na'imar ba, dan tun zuwanta bata zo ba.

Wani ashar Na'ima ta lailayo ta ajiye, jin wannan mugun ashar ya sa Abidah ta sake duban su, "Haba baiwar Allah, wannan ashar kamar ƴar maguzawa?".

Ƙugu Na'ima ta kame "Ubanki bamaguze".
Ajiye yaron hannunta ta yi jin ana neman zagar mata iyaye, "A'a baiwar Allah kada ki sake ki zagi iyayena fa".

Nan fa hayaniya ta kaure a falon, hayaniyar da jadda tajiyo ya sa ta fito dan ganin meke faruwa.

Nan fa abun ya dawo kan Jadda, Na'ima ta shiga surfa mata rashin kunya, ita kuwa Jadda shiru ta yi ta zubawa sarautar Allah ido.

Kwanci ta shi babu wuya, yau gashi muda kusan watanni uku a Kano, Momy Safiyya ta zo ta duba mu har sau biyu.

Dadyn Nazeer da kansa ya zo tafiya damu, duk yadda Jadda ta so ta hana hakan bai yuwu ba.

Mun sauka a Abuja lafiya, na so mu tsaya a gidan Momy Safiyya amma Dadyn Nazeer ya ƙi yarda.

Haka dai rayuwa ta cigaba da tafiya yau fari gobe baƙi,Momi Safiyya ta haifi yaron ta namiji idan ya ci suna Ibrahim Khalil shine suke kiram sa da Khalil,daga kansa bata sake haihuwa ba, ni kuwa yanzu yara na uku, dan nasake haihuwar yara biyu wato Bilal da Humaida wanda ake cewa Abida saboda sunan ƙanwa ke nan, shi yasa ma nasa mata sunan saboda na riƙa tunawa da ƴar uwata da ƙaddara ta raba ni da ita.

LAST FREE PAGE

Wannan shine taƙaitaccen tarishin mahaifiyar Nazbeer, amma cikakken tarishin ta da ma yadda suka rabu dan ƴan uwan ta guda biyu, duk zakuji sune acigaban labarin nan.

shin kunsan abinda su Hajiya Shuwa zasu magan ce, tunda karmu manta awancan lokacin da ta tura da sak'o tace akwai matsala fa, shin da ita da suwaye zasu had'u k'arfe hud'u,

kokuwa can b'angaren su Hajiya Turai da Hajiya Balaraba,
shin aikin Hajiya Turai zai iya cin Hajiya Balaraba ne koko ya abin yake tunda ga abinda Bokan nata yace,
ko ita Hajiya Balaraba d'in zata iya farga tagane cewa Hajiya Turai ba ƙaunarta take ba,
ko ita Hajiya Turai zata nasarar aurawa ƴarta T.j?.

Hmmm, akwai fa sauran cakwakiya domin yanzu wasan ya fara.

Game buƙatar cigaba da karatu zata biya kuɗinta naira 400 kacal  a sakata a paid group, da zarar kuma ya zama document za'a biya naira 500.

Za'a biya kuɗin ta wannan asusun👇

2297690395
Zainab Sani Laminu UBA bank
Shaidar biya ta nan 👇
08132135361

LOVE YOU ALL MY FANS💔💔

Taku
Abeedah✍️